[20/06 4:27 pm] Oum Hairan: *ZARRAH*

_Tare da Alƙalamin_

*_Oum Hairan_*

_Bismillahir Rahamanur Rahim_

_Page 3-4_

*_Wattpad-realfauzahtasiu_*

*_Telegram Link_*
👇🏻
https://t.me/joinchat/Gdtmu0TgTHu66CF7

______________________________
______________________________

Wani matsiyacin kallo yayi Mata ya watsar da ita sosai kalamanta sun Sosa zuciyarsa tunda yake baitaba katarin haduwa da tsageran daya taba duban tsabar idonsa ya fada Masa kwatankwacin wadannan tasassun kalaman ba sai wannan kucaka Kuma qazamar yarinyar almajira lallai ta daukowa kanta bala'in dazai addabi rayuwarta ko mutum me cikakken gata yace zaija dashi wahala yakesha balle matsiyaciya almajira da ko arziqin yar aikin gdansa batakai ba.
Juyawa yayi ya fice daidai lkcn da Inna ta bude idanunta ta saukesu akan Asma'u ta yafitota da

hannu ta matsa da sauri ta tsugunna tare da cewa “sannu Inna inane yanzu yakeyi Miki ciwo?" Girgiza Mata Kai tayi cikin muryar ciwo tace “naji sauqi Asma'ul Husnah meye yasaki kuka" sunkuyar da kanta tayi tare da saurin goge hawayenta tace “karki damu Inna zaki iya tafiya mu fita mu samu dan sahu mu tafi wani asibitin?" Zuro qafarta tayi ta miqe tace “zan iya Mana Asma'u dama sarqewar numfashin ne kawai Kuma yayi sauqi ince dai ba wanine ya sake farautar mutuncinki ba?" Murmushi ta qaqaro cike da tausayin Innanta tace “aa Inna muje gda zan baki labari yau na hadu da wani taqadirin dan iska da baisan darajar uwarsa ba bakiga cin mutuncin da yayi min ba harda Marina kawai don na tareshi ya taimakemu ya kawomu asibiti qememe dake dan dudun maguzawa ne yaqi  harda tukuicin baqaqen maganganu yayi tafiyarsa sai wanine ya tare Mana dan sahu mukazo nan asibitin ashe Wai na dan bamagujiyar nanne infadamiki yazo ya duba kowa yana ganina ya juya zai tafi nikuwa na rama maganganun daya fadamin nace indai bai dubaki ba kika mutu ya jira ZARRAH ta sai nayi shari'a dashi".....

Dariya Inna tayi ta lalubota ta rungumeta tace “ho ma'u na baki barin ta kwana do Allah ki rage zafin zuciya Kinga ke macece gdan wani zaki ki rinqa hqr da lamarin rayuwa kinji" cuno baki tayi gaba tace “waike waike Inna saikiyita cewa mutum yayi hqr Kuma mutanen duniya ba mutunci da hqr suka sani ba Ni kawai in anyimin ramawa zanyi idan mutum ya cika zaqewa nace ya jira lkcn da zan zama babbar likita wlh idan tsohuwarsa tazo hanuna allurar mutuwa zanyi Mata" Dariya sosai Inna tayi tace “Ma'ulele ma'un Inna tashi mu tafi kinji kar yazo yaci Mana mutunci" miqewa tayi ta Kama hannuta suka fito harabar asibitin cikin sa'a kuwa suka samu sahu suka hau zuwa unguwarsu Asma'u tabashi kudinsa a gurin bada kudin ma saida akaso ayi fada da dan sahu Saida Inna tasa baki sannan ta hqr suka tafi tanata mitar ita Inna komai akayi tace ayi hqr kamar wacce akayiwa wankan farko da ruwan alwalar La'asar🤣
Suna shiga gdan taci karo da Dije yar kishiyar Inna ta debo ruwa a bohol tana ganin Inna ta shige daki ta angije Dijangala ruwan ya tuntsire akan Lamunde dake tsugune gaban murhu tana hura wuta da bakinta, kafin kace kwabo kokawa ta rincabe tsakanin ita da Dije kiciki kiciki daqyar Malam Husaini dake shigowa ya raba fadan Dije ta tsaransa karya da gaskiya ya kuwa hau ya zauna ya dauki sanda ya shiga bugun Ma'u aikuwa ta angajeshi saura kadan ya fadi tayi waje ta zauna saman dakalin qofar gdan ta rinqa kuka.

Anan Saurayinta Sadiqu yazo ya sameta da qunshin kifinsa ya zauna yayita aikin rarrashinta daqyar ya samu tayi shiru shima Saida yace idan batayi shiruba mutuwa zaiyi aikuwa dake dama kukan na iskanci ne sai tayi shiru ta dago ta kalleshi tace “jiyafa a gabanka Dijangala ta angizani kwata na fasa qwauri sannan ruwana ya zube Amma shi malam babannan saboda suna bashi abinci baice Mata qalaba harma Kaine ka kaini chemist din Sallau shine yau danna rama ya Kama dukana Allah duk ranar da nacimma ZARRAH ta duk sai narama cutar da akayimin

Murmushi Saddiqu yayi yace “to Banda abinki Ma'una waye yake rama laifin mahaifa aisu sha kundum ne komai sukayi saidai ayi hqr abarwa Allah" harara ta galla masa tace “chabdi lallai ma Sadiqu Mai raken nan wato so kake kace na yafe makantar min da Innata da Lamunde tayi da ruwan zafi ko Kuma so kake kace na yafe hanamu abincin da baba yakeyi yake basu a boye duka Kai bari kaji harma satar kudi fah sukeyima Inna shiyasa na daina barin kudi a dakinmu nake baka kake ajiye Mana yawwa barima kaji yau da mukaje bara gdan Alh Qasim Dubu goma sha biyar yabamu kaga nasamu kudin makaranta na sauran musaiwa Inna magani musai kayan abinci ko?"
Numfashi Sadiqu yaja yace “kayy alhmdllh dama yau da tunanin kudin makarantar nan taki na yini Kinga yau har aikin gini nayi jiyama haka da ribar raken dana saro da kudin aikin ginin gaba daya dubu hudu da naira tamanin ne da so nake sukai sha hudu sai a biya kudin makarantar"
Jinjina Kai tayi tace “Allah Sarki dan Sadiquna kaga kasai siminti da kudinka tunda ai kaima naga gini kakeyi Mana wanda idan munyi aure zamu zauna yawwa nadai fada maka ka ginawa Inna ta daki qur'anin Allah bazan tafi nabarta anan su kashemin itaba kaga saura wata biyar yanzu muyi candy Kuma Mal yace da munyi Candy aure zaiyi mana dagani har Dijangala da Zabba'u, Inna ce mataketa qoqarin ganin ya barni nayi ko Hygiene ce shikuma yace baza'ayi yahudanci a gdansa ba"

Jinjina Kai Sadiqu yayi ya dauko Mata kifin daya siyo Mata ya miqa Mata tasa hannu biyu ta karba harda tsugunawarta tace “angode Allah ya dada arziki da wadata yasa wataran kasiye duk kifin garin nan" 🤔 zaro ido yayi sukayi dariya a tare yasa hannu ya dauki daya tace “ka qara Mana" girgiza Mata Kai yayi yace “ki shiga gda ki gyarawa Innanmu bari naje gurin musa na siyo Miki taliya ki dàfa Mana yau gwaggonmu taje qauye Kuma qila sai dare zata dawo" miqewa tayi ta shiga gdan ta tarar da Inna ta idar da sallar La'asar ta zauna zata farayi Mata surutu tace “Ma'u zanci qaniyarki akan sallah maza tashi kije kiyi alwala kizo kiyi sallah" dake tasan batada gsky Bata jaba ta fita ta dauki buta tayi alwala har yanzu fadan be qareba yanzu ma Saida ta harari Dijangala tace “zamu hadu a filin baja koli wallahi sai nayi qasa qasa nayi sama sama na dumbuli miya a ludayin uwar yarinya naga ubanda zai tare Mata shegiya me kan qotar gatari....."
Hadiye guntuwar maganar tayi Ikcn da taji saukar ranqwashi a tsakiyar kanta tana dagowa taga yayansu ne da take masifar jin tsoro don tasan yayi sukuwa a ruwan cikinta ba abune me wuya a gurinsa ba aikuwa kamar yasa kwado ya datse bakinta haka tayi muqus ta tashi sumsum ta shige daki ta fara jera sallolinta bayan ta idar yaro ya shigo ya kawo cefanen Inna tace a Ina tasamo cefane nan tayi Mata bayani dake Sadiqu ba baqo bane a gurin Inna yasa batayi fadaba tanajinta ta kunna rishow ta dora jallop din qamshi kuwa ya gauraye gidan Asma'u badai iya girki ba Inna tayi fama Amma tayi saa an iya da taimakon aikatau din da sukayi a gdan masu

kudi ita da innan yaron gdanne ya fara kawowa Asma'u hari dole tasa suka hqr da aikin suka fara wainar shinkafa da miya kafin iftila'in makanta ya fadawa Innah wadda tasa dole suka hqr domin Asma ita kadai bazata iyaba.

Lkcn data gama girkin ta zubawa Sadiqu nasa ta zubawa Inna itama ta zuba domin taci harta zauna zata faraci Inna tace “kin zubawa su Dijangala kuwa?" Turo baki tayi tace “ni gsky Inna kinayimin katsalandan cikin rayuwata su din bamu sukeyi naga ko yunwa zata kashemu ba sammana abincinsu sukeyi ba yanzu idan muka ajiye guntuwar da safe ai mayi dumame tunda ni makaranta zan tafi" murmushi Inna tayi cikin tausayin quruciyar yar tata tason ita duk abinda akayi Mata saita rama walau alkhairi ko sharri wanda rayuwa ba haka takeba tace,
Na haneki da barin yin ramuwa akan komai Ma'u rayuwa ta zahiri ba haka takeba kada ki zamo cikin mutane masu son dole sai sunyi qeqe da qeqe tabbas wadannan nau'i na mutane basa tsintar komai a rayuwarsu sai tarin nadama da danasani mara amfani to bandama quruciya irin taki Ma'u ai abinda ka bayar shine rabonka do Allah dauki kwano ki zuba musu inada naira dari biyu da safe sai baki dari kudin mota dari kisai abinda zaki karya kinji Ma'ulelena"
Janyo flat tayi ta zuba abincin kashi biyu ta dauka takai dakinsu Zabba'u ta tarar da Mama Jummai tana sallah ta dangwarar Mata da kwanon ta fice ta nufi dakinsu Dijangala ko sallama batayi ba ta dire kwanon tayo waje Lamunde da taya bera bari tace “kekam kin shiga uku da baqar rowa da nufinki muji qamshi a banza ko ho Ma'u albasa dai batayi halin ruwa ba" har ta bude baki zatayi raddi taga Yaya Mudan ya bude labule ya fito sumsumsum ta shige daki tana qwafa ta zauna  tanacin abincin tana qunquni takaicinta Yaya Mudan daya hanata rawar gaban hantsi shigowa yayi dakin ya dokanta harara tayi qasa da kanta yace “Ya Inna Ina abincin nawa ni?" Tasan halinsa sarai idan tayi wargi yanzu zata gwabzu hakanne yasata samawa kanta salama tanaji Inna tace masa “duba tukunyar ko ta rage" da sauri Ma'u tace “bari na zuba maka yaya" miqewa tayi ta dauki flat ta zubansa ta debe sauran a yar qaramar kula ta tura qarqashin gado ta koma ta zauna.

Yanacin abincin suna taba Hira da mahaifiyar tasu Asma'u najin haushin rashin zuciyar yayan nata duk matasan gdan sune suke ciyar da iyayensu Mata da qannensu Amma shi ko kudin omon da zaiyi wanki saiya tambayi Inna gashi da ƙi faɗin masifa"

Shi gani yake dole shi wata tsiyane qwafa tayi yakai Mata naushi ta goce yace “wlh Inna badan keba da tuni na dade da barar da yarinyar nan batada aiki sai jan maganar masifa shegiya kullum baqi take qarawa Wai kwananki nawa ma bakiyi wanka ba ne?" Turo baki tayi tana qunquni ya miqe yayi kanta Inna tayi saurin riqeshi tace “Kaga Mudansir ka kiyayi tabamin auta

qaniyarka zanci uwarme tayi maka da zaka wani zage kwanji kace zaka bugeta bakaganin ba qwari gareta ba" qwafa yayi yace “yawwa Inna wlh na qara ganinta da Sadiqu sai na kakkaryata nan Naziru abokina yazo yanasonta tayi masa rashin albarka har tana cewa nima din dana turoshi menene bare shi.
Murmushi tayi tace “to Banda abinka Mudan inakai ina shiga tsakanin Ma'u da Sadiqu Kuma ma meye laifin Sadiqu yarannan sunason junansu tun suna qananu bakace su rabu ba sai yanzu da aski yazo gaban goshi to ban yarda karna qaraji matuqar Ina raye saina dauki Ma'u nakaiwa Sadiqu dakinsa matsayin Mata insha Allahu na lura dagakai har babanku ba son zaman lfy kukeyi ba shikenan kowanne rashin albarkarku ya tashi akan Asma'u na zai qare yar tawa tilo bata damu kowa ba Amma kowa ya dameta"

Jinjina Kai yayi ya fice yana cewa “ai dama Mal yace kece kike daure Mata gindi a gdannan to Allah yasa na qara ganinta da Sadiqun a unguwarnan Kai nama daina zuwa ko Ina a qofar gidannan zan rinqa zama naga qarshen rashin kunyarki shegiya me idon aljanu" matsawa tayi ta kwanta jikin Inna tace “nifa Inna bansan me Sadiquna ya tarewa su Mal da Yaya ba dazuma da Mal yaganmu inaji Sadiqu yana gaisheshi yaqi amsawa nikuwa nace da Sadiqu dama ya daina wahalar da kansa aure ne dai dole a dauramin da wanda nakeso kamar yanda aka daurawa kowacce ya a gidannan ehe...."
Buge Mata haba Inna tayi tace “kinci malafar ubanki don qaniyarki bakisan cewa Allah uba yabawa damar zabawa yarsa budurwa miji ba to shine har kike wata taqama kul na kumaji yar jaka da qusa kawai tashi ki debi kayan makarantarki ki goge jiya Jiddah ma tazo bakyanan kinje debo ruwa tace ki taho muku ta tast book dinnan na biology zakuyi tast ranar laraba miqewa tayi ta fita  ta aro dutsen guga ta dawo tana gugar suna Hira da Innanta rabin hirar akan Aseem Shaheed ne da irin alwashin da taci na yimasa rashin mutunci duk ranar da Allah ya sake hadasu, Jinjina Kai Inna tayi tace “amma da kin hqr da yafi Miki kinga shi namiji ne ke kuwa mace ce ko marinki ya sakeyi ya cuceki a sadakinki sai an rage wani abu balle ma ni banga laifin da yayi miki ba badan dai sakarcinki ba mutum nawa kika nemi taimakonsu sukaqi taimaka Miki baki qullacesu ba saishi wasu ma mutuncinki suka rinqa farauta Amma duk kin manta saishi da yayi fada dake da fatar baki Kuma tabakin nasa ai ba kunyar gareki ba qila abinda kikayi Masa ma yafi Wanda kika fadamin"

Shiru tayi don tasan idan ta cika magana yanzu Inna zata gindaya Mata sharadi ita Kuma tariga ta qudurta a ranta saidai idan Allah bai sake hadasu da Dr Aseem Shaheed ba Amma saitayi Masa abinda zai tsaya Masa arai kamar yanda yayi mata ita ba lusarar ƴa bace dazai zageta yaci mutuncin Innanta kuma ta ƙyaleshi dama iya ita kaɗai yayiwa da da sauƙi kamar yanda na bayan sukayi amma shi Innanta fa yacewa tsumma tab ai wlh ya taro march kwararo kwararo zatake bi don ta ganshi tashin farko rotse zatayiwa motarsa idan yayi yunƙurin yin wani abu ta

kwankwatse masa yatsan ƙafarsa da dutse.
Dariya takeyi ciki ciki Inna tace “dariyar me kikeyi?" Saurin saita kanta tayi tace “tunawa nayi da wata tsokana da mukayi nida Jiddah a hanyar school ranar mun dawo dukkanmu bamuda kuɗin mota mukaga Mata da miji suna tafiya a qafa matar da tsohon ciki shine Jiddah tacemin lahh Asmah Kinga wata Mata ta haɗiyi wake ya kumbura Mata ciki nikuwa na matsa kusa dasu nace sannu Mata buhun garin kwaki kikaci ne yayi miki saqeqe a ciki  shine mijin ya Kama zaginmu muka mayar dashi mahaukaci mukayita dariya kawai saiya biyomu da gudu na turansa dutse ya tungule ya faɗi....."

Vote
Comments
Share

*_Oum Hairan_*
[20/06 4:27 pm] Oum Hairan: *ZARRAH*

_Tare da Alƙalamin_

*_Oum Hairan_*

_Bismillahir Rahamanur Rahim_

_Page 5-6_

*_Wattpad-realfauzahtasiu_*

*_Telegram Link_*

👇🏻

https://t.me/joinchat/Gdtmu0TgTHu66CF7

_______________________________

_______________________________

Daquwa Inna ta watsa Mata tace “wato dana hanaki tsokanar bakiji ba kenan aikuwa tabbas zan hadaki da yayanki yacimin qaniyarki ni banason sakarcin banza Shiru tayi saboda tsoran kada Inna ta fusata ta hadata da Mudan tasan kashinta tsaf zai bushe ta miqe sumsum ta nade kayan gugarta ta sanya a jakar kayanta ta fice ta dauki bokati ta tafi debo ruwa sawu uku tayi ta qyale kasancewar dare ya riga ya fara tana shigowa sallar Isha kawai tayi ta shimfida taburmarta ta kwanta tana addu'a bacci ya dauketa.
Da safe ta riga Inna tashi saboda zumudin kudin makarantar da zaa biya Mata tayi wanka aka dauki kwalliya aka dau jaka ta fito cikin shirinta tsaf Ma'un Inna idan taga dama yar gayuce ta gaske komanta qwas-qwas Amma idan taso iskanci tafi kowa iyashi dumamen taliyar data boye jiya ta dauka taci ta kora da ruwan koko ta miqe tace “inna zan tafi"
Fito da kudin Inna tayi ta miqa Mata ta qirga zari sha hudu ta miqawa Inna  uku da biyar tace "saura uku da biyar idan na dawo saimu siyo abinda zamuke ci kafin Allah ya kawo wata hanyar" Jinjina Kai Inna tayi tayi Mata fatan alkhairi ta fice ta nufi gdansu Jidda dake yafi nasu kan hanya nan suka dunguma suka tafi sunata hirarsu Asma'u na bata labarin irin wulaqancin da akeyi musu idan sukaje neman taimako sosai jiddah ke tausayawa qawar tata.

Da wannan hirar suka qarasa suka shiga aji suka fara daukar darasi Saida aka fito break sannan Asma'u ta nufi Office din Principal tayi sallama ta shiga principal din tanason Asma sosai saboda yanda malaman bangaren kimiyyar suke yabawa da qwazonta da ace makarantar tatace ma da tuni ta yafewa Asma kudin makaranta saidai kash batada iko.
Rusunawa tayi ta gaisheta ta amsa sannan ta fito da kudin makarantar ta miqa Mata tayi rubuce rubucenta ta miqanta receipt ta miqe har takai bakin qofa taji a bayanta ance “Asma'u Hussain" tsayawa tayi adan tsorace tace “yes mAh" murmushi tayi tace “meye yasa duk biyan kudin makaranta kece qarshe ne meyesa iyayenki sukewa karatunki ruqon sakainar Kashi bayan Kuma Ubangiji ya Basu dama domin yabasu ke me qwazo da son karatu?" Idanunta ne ya kawo ruwa tayi saurin daukewa tace “na gode mAh kawai ta juya ta fice daga office din principal din  ta nufi inda sukecin abinci yau batada ko sisi sai kudin motarta don haka ta nemi guri nesa

ta zauna tana kallon daluban wani na siyan wainar fulawa wani na siyan cake kowa dai da abinda yakeso. Jiddah ta hango ta nufota ta zauna kusa da ita tace “yadai naganki anan" dubanta tayi tace “to da Ina kikeson ganina?" Share zancen jiddah tayi da cewa akwai wani guy dana tama a bayan makarantar nan yau indai mun ganshi saina goge Masa hadda"

Zaro idanu Asma tayi tace “kayy Kinga ki rufa Mana asiri Principal tace mu daina kula mazan bayan makarantar nan yawancinsu duk yan shaye² ne" harararta Jiddah tayi tace “kefa wani lkcn farar kura ce me suka Isa suyi Mana basai mu gudu ba mu jasu har area mu hadasu dasu Sadiqu suci ubansu" Shiru tayi tana nazarin kalamanta kafin ta dago tace “nidai Babu ruwana bazanje garin goge musu hadda su su gogemin tawa ba" dariya Jidda tayi tace “bansan yaushe kika zama matsoraciya ba wlh Ma'u Allah ya shiryeki" bata Kuma cewa komai ba har suka koma aji Basu suka tashi a makaranta ba sai uku Wanda a qa'ida biyu suke tashi wani mugun malaminsu ne yabasu assignment me wahala shine suka bata lkc haka gashi yace a lkcn yakeso dukkan fuskokin daluban daka gansu kasan sun jigata da yunwa musamma Ma'u da batayi karyawar kirki ba gashi babu kudin break sun riga kowa something suka fito duk ta galabaita suka nufi get megadi ya Kuma taresu akan cewa principal tace kada su fita da daidai su bari su tashi gabadaya,

Neman guri sukayi suka zauna kawai Jidda taga qawar tata na kuka Asma'u babu juriyar yunwa ko kadan tasan dalilin kukan don haka ta miqe da sauri ta nufi shagon me gadi ta siyo musu biscuits pure blues dan saba'in ta siyo musu lemo jarka daya sukaci Saida sukaji dama dama asmai ta dubeta tace “dama kinada kudi shine kikaqi ki siya Mana break?" Harararta Jiddah tayi tace “wanne kudi ke gareni kudin motarmu ne naga zaki mushe na taimaka na siyo Mana muka taba Kinga malama an gama fitowa kawai miqe mu yanki burtali"

Takaici ne ya hana Asma'u magana saboda tana cika magana zuciyarta fadowa zatayi haka suka rinqa dabawa a qafa gashi da nisa tsakanin unguwarsu da makarantar sosai suna tafe Jiddah nayi Mata hirar tura haushi taqi kulata sunzo daidai wani guri da ruwa yake taruwa kawai basuyi aune ba sukaji ruwan dagwalon kwata ya fallatso musu ya bata musu jiki musamman Asma'u da ruwan yafi batawa ta sunkuyar dakai ta kalli kanta tun daga sama har qasa ta dago kanta ta sauke akan motar da aka tayar ana Shirin tafiya zuciyarta na azalzala taga me motar yaja zai qara gaba ai batayi wata wata ba ta dauki wani dutse qato dake gefensu ta jefi motar akwaita da mahaukacin saiti kuwa ji kake taratsatsa glass din bayan 4matic din ya tarwatse hakan yasa me motar cin uban birki a fusace na kujerar me zaman banza ne ya fara

fitowa daidai Ikcn data nufo gurin itama tana fadin “ba iyanan naso ya tsaya ba sonayi ya ishe kan daqiqin dakejan motar yayi masa Ramin da jini zai hade da qwaqwalwar shege muga ta gadara da dagawa...." Sauke tafin hannunta tayi a fuskarta jin shu'umin Marin da aka dauketa dashi ta Jima dafe da kuncinta kafin tayi qarfin halin dagowa tana tuna Marin da Aseem Shaheed yayi Mata jiya kwatankwacin azabar da taji kenan aikuwa tabbas saita rama wannan koma uban waye ya daga hannu ya Mari fuskarta me daraja,
Idanunta ta rintse ta dage ta daukeshi da Marin da shima Saida ya dafe gurin kafin ya dago ta sake sauke Masa wani ta daga hannu zatayi na uku Wanda ya fara fitowar ya riqe hannunta da sauri jikinta na bari ta bude idonta daidai Ikcn da Dr Aseem ya bude nasa shima tar a kanta lebensa datse da haqoransa ya saita injin idonsa akanta tare da sanya hannunsa ya zame hannun Zahran daga nata ya riqe na yan sakonni sannan ya saki Yana qara kallonta itama shi take kallo cike da mamaki da Kuma tsana.

Kafin yayi mgn tayi da cewa “au dama Kaine shaidanin daya batamin uniform dina lusari kawai kagani dai kaga irin aikina dama Saida na fada maka zamu sake haduwa gashi kuwa mun hadu ko banza zuciyata ta dan sauka daga radadin
Daka Bata sauna kawai ka dauka ana tabani aci bulus ne jiya kaci mutumcin mahaifiyata da tafi taka uwar don alamu sun nuna kaikam taka jefar dakai tayi wata me tsautsayin ta tsinta.
Sannan yauma ka batani da ruwan kwata Kuma kayi tunanin wuccewa salin alin haba yaro kayi kadan ka taba ma'un Sadiqu ma'un Inna ka zauna Ify gashinan kayi ta glass din motarka Kuma dole aje akaiwa me gyara yaci kudi nidai nasan ko kaina ka siyar bazai gyara maka ba......
Tana maganar tana qasa qasa da hannunta ta sake daukan wani dutsen me nauyi tayi kamar zata wucce kawai ta sakar masa a babban yatsansa yakuwa yi qasa da sauri tare da sakin wata siririyar qara kafin Zahran ya Ankara ma'u takai a dari da sittin ba Zahran ba hatta Aseem da jini yake ambaliya a qafarsa Saida ya dago ya dubeta Ikcn da take cewa su Corona virus aje ayi treating kafin mu sake haduwa na daujeta Wawa da kace bakaji.........

Vote
Comments
Share

*_Oum Hairan_*
[20/06 4:27 pm] Oum Hairan: *ZARRAH*

_Tare da Alƙalamin_

*_Oum Hairan_*

_Bismillahir Rahamanur Rahim_

_Page 1-2_

*_Wattpad-realfauzahtasiu_*

*_Telegram Link_*
👇🏻
https://t.me/joinchat/Gdtmu0TgTHu66CF7

______________________________
______________________________

_Farkon labari_

_1/3/2007_

Harabar gdan attajirin cike yake da mabarata maza da Mata yara da manya kowannensu yayi jungum jumgum Yana tsumayin fitowar Alhaji Qasim Wanda ya kasance shine mamallakin gdan Wanda ya kasance baya goya marayu jarumi Kuma adali me taimako da taimakon Allah da'ira da'ira almajiran sukayi kowa yana tattaunawa da abokin shawararsa inda a can nesa kadan da

mutanen na hangi wata dattijuwar makauniya da wata yar kyakkyawar budurwa da shekarunta bazasu haura 17 ba sanye take da hijjab ruwan qasa Wanda dadewa da kodewa tasashi dole ya koma toka toka rigarta da zaninta ma gambal habaru ne ma'ana wari da wari tanada matsakaicin tsayi duk da kasancewarta a jigace Kuma a wahalce kallo daya zakayi Mata kasan alamu sun nuna tana tsananin ji da wannan mahaifiya tata fiye da tunanin Mai tunani.
Ba fara bace kallon farko zakace Mata baqa saboda dauda da rashin samun nutsuwar kula da Kai saidai idan ka qura Mata ido zaka gano cewa ba baqar bace kamar yanda idanu ya nuna a farko saboda roɗi roɗin hasken da zakake hangowa ta wasu bangarori na jikinta, tana da fasali da diri na bam mamaki Wanda a qananun shekarunta zakayi al'ajabin qirar da ilahi qadiran ala mayyasha'u yayi Mata so dake lamarin Allah yafi gaban misali da mamaki dole ka aje tunaninka ka Kama abinda ke gabanka.

“Asma'u! Asma'u!! key Asma'u!!! Tunanin me kikeyi ne dalla malama tun dazu Alh sai miqa Miki kudi yakeyi...." Abinda ya dawo da ita hayyacinta kenan ta durqusa har qasa ta karba ta bude baki cikin siririyar muryarta tace “mun gode baya goya marayu Allah ya tsare gabanka da bayanka ya hana maqiyanka ganinka sai bayan ka wucce Allah ya tare maka zafin hassadar maqiya da mahassada ta koma kansu....." hakanan ta rinqa jero addu'ar kamar yanda takanji Ummah tanayiwa duk wanda yayi musu ihsani.
Dadin addu'ar da Alh Qasim yaji tasashi qara zarar naira dubu goma ya sake miqa Mata kawai saita fashe da kuka bayan ta karba tayi masa godiya da fatan alkhairi, ya wucce ita Kuma ta dugungune kudaden ta tura a bra dinta ta Kama hannun Ummah tace “Ummah yau Allah ya dubemu ya amsa addu'ar ki ta jiya ya kawo Mana dauki dama tunda muka fito nake tunanin idan bamu samu sadakar Nan ba yau Ina muka Kama bamuda abinda zamuci ko na garin kwakin yau babu gashi gobe ance kar naje makaranta idan ban kawo kudin tearm ba, nikam Ummah badon kince na daina roqonki ba da sai nace kiyi hqr ki mayar dani makarantar gwabnati tunda na samu horon farko a ta kudin Ummah kudin sunyi yawa 14 thausand per team gashi babu mataimaki a gareki sai Allah da bayinsa zababbu...."
Lalubo bakin yar tata tayi tace “Asma'u komai kikaga ya faru da sanin Allah kada ki damu ba wayonmu ko dabararmu ke rayamu ba burina ko bana raye kiyi karatun bokon nan me zurfi kema kamar yanda kikekan na addini Asma'u burina ki zama likitan ciwona saboda na fara gajiya da wulaqancin da likitawa sukeyi Mana duk lkcn da ciwona ya tashi muka rasa mataimaki Asmah bani da tabbacin amfanar karatunki Amma inaso ki amfanar da al'ummah don Allah kada rudin duniya yasa kema kibi wancan sahun kinji?"

Jinjina Kai tayi cikin qoqarin sanyawa kanta dakiya da juriya nason cikawa mahaifiyarta burin data rayu dashi taqici taqi sha dominta ita kadai ta hana kanta sukuni dominta, da wannan tunanin ta Kama hannun Ummah ta miqar da ita suka fara fita daga harabar gdan suna tafe

suna taba yar hirarsu tsakanin gdansu da gdan Alh Qasim tafiyace miqaqqa Amma haka ummah tace su tafi a qafa kawai don tsoron kada tayiwa kudin makarantar yar tata gibi ta shiga wani yanayi suna tafe suna Hira har sukaci Rabin tafiyar sannan suka tsaya saboda nishin da Asma'u taji mahaifiyar ta ta fara ta riqota da sauri ta zauna ta kwantar da ita a jikinta tace “Ummah kingani ko abinda nake gudu kenan shiyasa nace mu hau dan sahu naira dari zasu kaimu kikaqi....."
Mgnr ce ta maqale cikin tashin hankali ta rinqa jijjigata tana Kiran sunanta Amma Ina ta Suma nan fah Asma ta dora hannu aka ta kurma ihu tana cewa wayyoh Jama'a a taimakeni Ummana zata mutu don Allah kada ki bari ta mut...." Nandanan saiga mutane sun taru a gurin masu fifita nayi masu surutu nayi, itakuwa titi ta bazama ta fara tsayar da motoci da yawansu basa tsayawa wata mota tazo zata wucce tayi tsalle ta dira gabanta tare da rintse idonta take me motar yaci wani uban birki ji kake qiyyyyyy, abinda yaja hankalin kowa dake gurin kenan suka juyo domin ganin meye yake faruwa Asma da take tunanin ba a wannan duniyar take ba ta bude idonta daidai lkcn da taji an dauketa da wani gigitaccen mari daya sanyata durqushewa a qasa yace “banza mahaukaya zakizo kijamin masifa a banza......" Riqe qafarsa tayi da sauri tace “don girman Allah kada ka tafi ka taimakamin kada Ummah na ta mutu a titi kakaimu asibiti....." Dagota yayi kamar abin arziki ya qare Mata kallo sannan yayi watsi da ita tare da jan tsaki ya nufi inda Ummah take kwance ya leqa,

Tunaninta ya gama bata taimakonta zaiyi taga ya nuna Umman da yatsa yace “dama akan wannan tsumman kikeson kiyi asarar taki rayuwar sakarya kawai to meye yayiwa wannan yamusasshiyar tsohuwar saura ai bazata warke ba qarama ki lallaba taki rayuwar qila tayi Miki amfani a gaba farin magi duk ya kashe tsohuwa" durqushewa ta kumayi a qasa tana qoqarin yimasa magiya ya fincike qafarsa yace “stupid girl banida lkcn batawa akan wannan gawar...." Da wannan kalmar ya fada motarsa ta miqe tana me binsa da kallo tare da Jinjina Kai daidai lkcn Allah yakawo wani dan sahu wani mutum ya tareshi suka tarairayi Ummah suka sakata a ciki suka nufi Asibiti mafi kusa dasu da niyyar abata taimakon gaggawa kafin su tafi gda.
Suna zuwa aka tura Ummah aka shiga da ita ciki suka sanya mata ruwa kafin fitowar babban likita, bayan kamar shudewar awa guda sai gashinan dauke da files a hannunsa ya nufo dakin ta zuba Masa ido cike da wata muguwar tsana shima yana ganinta yaji gabansa ya fadi yayi saurin mazewa tare da juyawa ga daya gadon Yana duba mara lafiyar ya dauki file din yayi rubuce rubucensa ya juya zai fita tabisa da sauri tace “Dr Aseem wannan karon ba alfarma nake nema ba da kudina na kawo mahaifiyata asibitin nan domin a dubamin lfyrta qila taka uwar bata sallama farin cikinta domin nakaba shiyasa kake kallon iyaye Mata a banza koma dai menene kada ka manta ta haifeka ta raineka har zuwa yanzun Bata daina baka shawara ba inhar tana raye just aikin kudi kakeyi a biyaka kazo ka dubamin uwata nasan bakada ikon canza qaddarar Ubangiji Amma kayi wani Abu da zaisa naji a Raina bakada hannu wajen rushewar rayuwata wlh idan ka bari sakacinka ya kashemin mahaifiya sainayi shari'a dakai duk ranar da ZARRAH ta takai inda mahaifiyata ta bata darenta da ranarta domin ganin takai.........."

Wani murmushi yayi me kama dana rainin hankali ya matso gabanta ta matsa ya tsaya a inda yake yace “au kenan har jiran ranar ZARRAR ki kikeyi Kuma kinaji a ranki zaki sameta okay almajira kin birgeni da kika taro wasan dani saidai inaso ki sani bakikai na farashi dakeba ki bari ZARRAR taki takai tukun samu fara takun dake am bari kiji wani Abu daga kallonki naji na tsaneki saboda idanunki sun nuna bakida tarbiyya wannan dalilin yasa naji bazan taimakeki ba bazan taba taimakonki ba yarinya wannan asibitin nawane saboda haka na baki 10 minutes ki debe tsummar tsohuwarki a qara gaba kar a zubamin qwarqwata" hannu yasa aljihunsa ya zaro raffers ta dari biyar biyar ya jefa Mata yace “ga wannan idan ta mutu a sai geron sadaka" cafewa tayi ta saita tsaiwarta har ya juya zai tafi ta daga murya tace “Aseem Shaheed" juyowa yayi da sauri jin ta ambaci cikakken sunansa ta matsa gabansa ta keta raffers din gda hudu ta watsa masa tayi murmushi me hade da kuka tace “Sunana Asma'u Hussain ka rubutani cikin qaddarorin da zasu addabi rayuwarka wlh saina baka mamaki matsiyaci me taqama da kayan aro shashasha Wawa kada ka damu zamu sake haduwa a gaba wasan baa faraba"........

_Hmmmm Wasan baa fara ba correct Asma'u  Dr Aseem a sake shiri_

*_Oum Hairan_*
[20/06 4:27 pm] Oum Hairan: *ZARRAH*

_Tare da Alƙalamin_

*_Oum Hairan_*

_Bismillahir Rahamanir Rahim_

_Page 7-8_

*_Wattpad realfauzahtasiu_*

Telegram
👇
https://t.me/joinchat/Gdtmu0TgTHu66CF7

______________________________
______________________________

Wata zazzafar ajiyar zuciya ya sauke Ikcn da yasa tisue yake tsane jinin tare da rufe ciwon sosai dutsen ya shigeshi hakance tasa Bai iya jan motar ba sai Zahran ne yaja Kai tsaye suka nufi Asibiti anan Zahran yayi masa dressing na ciwon.
Duk dagowar da Zahran zaiyi sai yaga shi yake kallo har ya gama Masa yace “angama Dr yau ka gamu da sharrin yayan talakawa narasa me muka tare musu sukejin haushinmu nasan da zaa Basu dama zasu iya kashemu su hut....” daga Masa hannu yayi a fusace jikinsa na yace “ka nemomin gdansu yarinyar nan a duk inda take a fadin garin Kano" da sauri Zahran ya Mike yace “in kasan gdansu me zakayi Mata" ya dade yana kallon Zahran kafin yayi murmushi ya miqe yace ya fara tafiya yana dingisa qafa yace.

“Nasan ba kowa bace ita face almajira mabaraciya yar jagoran makauniya so inason sanin asalinta need saboda nayi ramuwar gayya da hujja tabbas ko Ina yafe komai bazan yafe laifin fitarmin da jini a jikina ba hannun daya dauki dutse ya fasamin yatsa ya ciremin farce saiya goge takalmina" ficewa yayi ya shiga motarsa ya fuzgeta da mugun gudu ya nufi unguwarsu dake Shagari quarters yana parking ko rufe qofar baiyi ba ya nufi cikin gdan ya bude parlourn ya shiga Mimee matarsa dake zaune da cup a hannunta ta miqe da sauri da niyyar taroshi ganin Yana dingisa qafa yasata dafe qirji tace “Na shiga uku Life meye ya sameka a qafa?" Kallonta kawai yayi ya wucce dakinsa ya fada gado yana huci kamar yaci Babu tunda yake Babu mahaluqin daya taba karambanin daga hannu ya mareshi har mari biyu a Ikc daya da sauri ya miqe tare da kallon qafarsa cikin wani mugun quncin zuciya yake furta “Wacece ce ita meye take taqama dashi wacece ita!?" Yana mgnr ne da qaraji abinda yasa Mimee shigowa da sauri tace “Ify Life?" Iska ya furzar tare da cewa da ita  “Asma'u Hussain wacece Asma da ta iya daga hannu ta mareni wacece ita data fitarmin da wani bangare na jikina?"

Duban qafarsa yayi tare da cewa “wlh saita gane kurenta saina koya Mata hankali saina wulaqantata ita da danginta gabadaya saina rusa Mata burikan rayuwarta" fuuuu ya shige bathroom Sarai Mimee tasan halinsa idan yanakan tsini bajin rarrashi yakeyi ba shiyasa batayi yunqurin rarrashinsa ba ta nemi guri ta zauna da tunanin meye ya hadosa da mace shida magana ma ko da maza ba damunsa tayi ba da har takaisu ga wannan tsamar tabbas bayan tiya akwai wata caca banza batakai zomo kasuwa.
Miqewa tayi ta fita ta hado masa abinci don tasan ba fitowa zaiyi ba yau an taba mazan fama Aseem rikici ne gabadayansa tunda ya dauki ragamar ramuwar Nan to gara tayi masa fatan nasara don idan ta cika mgn kanta fadan zai dawo. Zama yayi yana tsane jikinsa yace “meye wannan din?" Murmushi tayi tace “bansan zaka dawo da wuri ba jallop din taliya ce" zuba masa ta farayi ya karba Yana tauna abincin kamar Yana tauna magani ajiye flat din yayi ya miqe a gado tana kallonsa yanata qwafa ganin bazata iya ba ta miqe ta debe kayan ta fice dasu ta hada me aikinta dasu ita Kuma ta shige dakinta itama ta kwanta.

Wayarsa ya janyo ya kashe don yasan zaayita kiransa a hospital Kuma ba iya zuwa zaiyi ba yau gabadaya Asma'u ta Bata Masa lissafin ranar dole haka zata tafi a banza. Haka ya yini kwance saidai daganan ya juya nan sallah kadai ke tashinsa hudu da rabi na yamma Zahran ya kirashi yace “ya fito yanada Ibr game da aikin daya sanyashi" miqewa yayi ya dauki rigarsa yasa ya dora hula ya fito a harabar gdan ya ishe Zahran ya qarasa fuskarsa kamar ta sa tsabar damuwa mota ya bude ya shiga suka dubi juna Zahran yace “Kamar yanda ka fada Sunanta Asma'u Hussain Babanta  Mal Hussain talaka ne na qarshe domin kuwa tunda ya taso aikinsa Bai wucce dako da faskare ba mahaifiyarta Amina itace babbar Matar Mal Husaini sai sauran matan babanta su biyu Lamunde da Lantana su Hudune Yaya a gidansu Mudansir sai Zabba'u sai Dijangala sai ita qarama Asma'u wadda ake Kira da Ma'un Inna ko ace Ma'un Sadiqu autace a gdansu duk da kasancewar uwarta ba komai bace a gdan Amma hakan bai hanata samun gata daidai na talaka ba duk da kasancewar Babu abin sisi da Mal Husain yakewa yaran saidai suyi sana'a da iyayensu suyiwa kansu ita Inna da kake ji macece me qoqari gaya akan yayanta tayi qosai tayi aikatau gdan masu kudi tayi surfe tayi dakau sannan tayi wankau zamanin tanada idanunta har abincin siyarwa tayi duk da tanada ya mace Bata Dora Asma'u talla saidai Mudan da ita su dauka suje su siyar a bakin kasuwa a cewarta ita ya mace kadara ce me tsada Kuma abar farauta ce idan kayi wasarairai da ita kamar dawisu take inda yafi yalwal bishiyoyi da Ni'ima nan take fakewa tace zatayi rayuwa a cikinsa idan akayi rashin saa sai asamu mafarauta su kameta shikenan rayuwarta ta lalace:

Yarinya ce me qwazo tun tana qarama hakan yasa uwarta taci burin sai tayi karatu me zurfi Ikcn da aka makantar da Inna Ikcn Asma'u ta gama primary daganan abubuwa sukayita lalacewa dan abinda ake fita a Nemo na rainawa babu halin fita a nemoshi Nan suka shiga Ni yasu

abinda zasuci ma yakan gagaresu akwai wani yaro Sadiqu da tun tasowar Asma'u yakeyi Mata wahala shine rakata makaranta shine komanta saiya zamana idan yasai da rake ko ya dauki tallan yalon bello yaje ya siyar ne yake samu yabasu abinda zasuci.
Ana hakane wata Ladi almajira tayiwa Inna tayin fita bara tunda dai Allah yasani batada mataimaki da farko Inna taqi abin Amma Ikcn da Asma'u ta farayi mata mitar duk qawayenta sun tafi makarantar secondary ita tana gda saita farabin Ladi bara suna samo na batarwa a hakadai har suka Tara kudin makarantar Ikcn har anci zango daya suka kaita Prime school dake Inna tun dacan Bata yarda yaranta sunyi makarantar gwamnati ba  tace Babu karatu ita Kuma so take yaranta suyi karatu, daga Ikcn da Asma'u ta fara zama budurwa saiya kasance idan sunje neman taimako mutanenmu sai suka fara nuna maitarsu akan yarinyar itakuma uwar tana nuna Mata aibin hakan musamman dake Asma'u tana zuwa islamiyyar dare, matsalar Asma'u daya ita tun tana qarama batada hqr Kuma Bata yafiya indai kayi Mata saita rama so da mutane suka fara gwada rashin imaninsu akan mahaifiyarta sai ta dauki gabarar duk Wanda yayi Mata ko waye a duniya saitayi Masa kalmarta daya itace “ka jira ZARRAH ta ranar da zan zama babbar likita zanyi fada da uban kowa a duniya Kuma zan nuna maka kaiba komai bane" yanzu haka zancen da nakeyi maka burinta na gab da cika domin kuwa takusa kammala secondary Wanda Innarta tafi shekara biyar tana adashin gata domin Asma'u ta wucce makarantar da zatayi karatunta na likitanci"

Murmushi Dr Aseem yayi yace “aikinka yana kyau Kuma meye yanayin ubanta da kudi sannan a wacce unguwa suke zaune?" Jinjina Kai Zahran yayi yace “wanda yayimin bayanin tarihinsu yace kirarin mahaifinta Mal Husaini idon cin naira indai kanada kudi to kanada cikakken mutumci a gurinsa idan kuwa baka dashi to kashinsa yafika daraja anan Tukuntawa gdansu yake shikuma babanta a sabuwar gandu majalissarsu take gefen rumfar wani me nama suna zaune idan ansiya suyi sudi aikinsu kenan"
Jinjina Kai Aseem yayi yace “ka gama magana inason kwadayayyen mutum saboda buri yana saurin cika Asmah ki jirayi zuwana burinki bazai taba cikaba zan rusanki duk wata walwala da farin ciki zaki rayu da qunci zan massheki baiwa a gdana saikin lashe tafin qafata da harshenki...... Dafashi Zahran yayi yace “tabani haushi dazu Amma da naji tarihinta sai tabani tausayi please ka hqr da daukar fansar nan kabarta don Allah akwai quruciya yarinya ce qarama fah....." Hannu ya Dora Masa a baki yace “karka qara bani hqr wlh bantaba tausayin wani Abu kamar yanda na tausayawa yarinyar nan ba Amma hakan bazai hanani daukar mataki akanta ba saita Raina kanta Kuma sai tasan tasa Wasa da Aseem Shaheed"...........

Vote
Comments
Share

*_Oum Hairan_*
[20/06 4:27 pm] Oum Hairan: *ZARRAH*

_Tare da Alƙalamin_

*_Oum Hairan_*

_Bismillahir Rahamanir Rahim_

_Free Page 9-10_

*_Wattpad realfauzahtasiu_*

Telegram
👇
https://t.me/joinchat/Gdtmu0TgTHu66CF7

Tunda Asma'u ta koma gida take zumbure zumbure Matan gdan Babu Wanda ya kulata Inna kuwa ba ido ba balle tasan matsalar yartata haka tayi wanka tayi sallar azahar da La'asar ta zauna tsince wake bayan ta gama ta dora musu abinci tana girkin tana qunquni da haka ta gama ta zuba ta zauna tanaci bayan ta gama ta shirya ta tafi islamiyya sai shidda ta dawo Ikcn uniform dinta ya jiqu ta wankeshi ta shanya sai Ikcn ta jirge ta zauna tana bawa Inna Ibrn abinda ya faru.
Sosai Inna ta nuna rashin jin dadinta da abinda yartata tayiwa Aseem tare da rufeta da fada daga baya ta dawo yimata nasiha to ta danji a Ikcn ta miqe tayi sallah ta kwanta, washegari da wuri ta fice saboda so takeyi yau suje makarantar da wuri cikin saa ta tarar da Jidda ta shirya suka tafi suna tafe suna Hira Jidda tace.
“Nifa jiya kin kullemin Kai Asma'u waike bakida tsoro ne baki tsoron kada mutumin nan ya sanya yan sanda su kamaki?" Tsaki tayi tace “kuma saboda Ina tsoro saina bari yaci mutumcina na qyaleshi ko?"

Kada Kai Jiddah tayi tana Shirin yin magana wata mota tazo ta giftasu kawai sai sukaga taci burki a gabansu hankalin Asma baa kan motar yake ba har zasu gifta taji Jidda tace “mun shiga uku Asma'u mutumin jiya ne fah" da sauri ta kalli gurin suka hada ido ta galla masa harara ta qarawa tafiyarta sauri saboda Inna tace idan ta sake kulashi sai taci mutuncinta.
Murmushi yayi cike dajin tsanar yarinyar a qasan zuciyarsa yaja motarsa ya qara gaba ta gefenta ya wucce shuuu taja fasali tace “kaci arziqin Inna ta hanani kulaka wlh yauma dasai nayi maka rotse sakarai Wawa"

Duk da Aseem baiji abinda ta fada ba Amma ya fahimci dashi take murmushi yayi ya qara bawa motarsa wuta tabbas sai yayi maganin rashin kunyar yarinyar nan da take ganinta daidai dashi saiyabi ta kowacce hanya yaga ya koya Mata hankali saiya sanya Mata jin cewa Ashe ita ba kowa bace a rayuwarta tunaninsa yanzu ta inda zai fara gudanar da aikinsa kisan mummuqe yakeson yimata batare da wani ya gane qudurinsa ba yakeso ya baje tarihin rashin kunyar Asma'u,
Yana tuqi yana murmushi Yana maimata sunanta yanayin yanda ta harareshi dazun yana Masa gizo yanajin wani nishadi da Allah yasa yarinyar ta siyar Masa da qasar wasan dole akwai badaqala zai ganar da ita kurenta na shiga sharafin daba nataba. Koda yaje asibitin ya fara duba marasa lfyrsa bayan ya gama ya wucce nasa private hospital nanma yayi abinda zaiyi sannan ya shige office dinsa ya zauna yana juyi a kujerarsa cike da zumudin ganin yamma tayi Zahran ya gama aikinsa ya daukeshi suje su nemi mahaifin Asma'u kamar yanda ya tsara kafinnan Saida ya sake tura wani yaronsa yayi masa binciken tsaf inda anan ne yaron nasa Uzairu yake sanar dashi ai Mal Husaini yasa gdansa a kasuwa zaiyi auren yaransa uku sukuma iyayen zasu koma qauye da zama wacce bazataba Kuma tasan inda dare yayi mata.

Fiye da tunani Aseem yaji dadin wannan farin lbr aikuwa hudu da rabi suka fice daga asibitin suka nufi bakin kasuwar sabuwar gandu inda anan Mal Husaini yake zama Nan suka nemi a rakasu ofishin dillalan qasa akayi musu jagora sukaje suka gaisa Zahran yana nunawa Aseem Mal Husaini da yaketa maka hamma da hularsa ko Kari Babu bisa dukkan alamu yunwa yakeji.
Caraf kuwa Alh Bala dillali yace “Idon cin naira da alamun dai yau baa sammaka abin sawa a maqoshi ba ka fito" kamar me jiran kadan ya balle zance kamar Wanda ya qone a tsakiyar ka cewa yake “yo dama wadannan sakarkarun waye yanzu yake sammin abincin Lantana da Lamunde sunce sun daina cida qato Wai auren yayansu zasuyi Amina ce me tausayina take bane to itanma saidai idan wannan ja'irar yarinyar Ma'u batanan amma fir take hanawa tace ai ba Basu nakeyi ba kuma tana ganin lkcn da nake bawa Lamunde nikuma ganin suna fita bara nasan na annabi baya qarewa shiyasa bandamu da sammusu ba gashi anma kasa samun me

siyan kangon can nawa bare na Dan murmure kafin bikin nan"

Jinjina Kai Aseem yayi Bala dillali ya dubesu yace “Alh Allah gida ko fili ko kango ko haya ake buqata?" Cire hularsa yayi ya maida hankalinsa ga Zahran Zahran ya gyara zama ya karkace yace “gda muke buqata ginin gargajiya anan Tukuntawa zamu zuba shanu da tumaki a ciki...." Yunqurowa Mal Husaini yayi Mal Bala ya dakatar dashi yace “toh ikon Allah kamar Kuma na nawa kuke buqata?" Kallon Aseem Zahran yayi Aseem da sai yanzu yaga samar mgn yace “ba qarami ba ba babba ba duk yanda kasuwa ta Kama munaso idan akwai a nuna Mana abune na urgent da muke buqatarsa tsakanin yau da sati biyu" duba Mal Bala yakai ga Mal Husaini da dama yake jiran abashi dama nan yayi kwance kwance yace “yo Alh Allah muje suga nawa Mana ko Allah zaisa a daidaita tunda qananun masu kudi sun kasa siye sunce zaici kudi wajen gyaransa

Tunda ya fara mgnr Aseem ya zuba Masa ido har ya gama murmushi Aseem yayi Wanda shikadai yasan dalilin murmushin nasa yace “ok muje mu gani idan yayi sai muyi ciniki Amma gsky muna buqatar gurin da wuri zamuyi aiki a ciki ne" Babu tunanin makomar iyalai Mal Husaini yace “Haba yaro abinda yake kasuwa ai ko yau kakeson abinka baka akayi indai ka biya nidai fatana Allah yasa gurin yayi maka fitinar zabba'u ta isheni yau ta debo wannan gobe ta kwaso wancan gara na auraddasu kawai na huta sauran kudin naci tsire dasu hhhh koba hakaba yaro..."
Sudai murmushi kawai sukayi suka nufi motar Mal Bala da Mal Husaini suka shiga baya Aseem da Zahran suna gaba a haka Mal Husaini yaketa basu kwatance suna amsawa har suka shiga unguwar tun daga farkonta suka fara Raina kansu asalin uguwar talakawa ce ko Ina kwatami ne yake gudu haka sukayita kutsawa lunguna har suka isa qofar wani tsohon gda ginin jar qasa dako arziqin yabe bai samu ba babu qofa a gidan sai labulan tampol da aka sanya domin sakaye gdan, tundaga qofar gdan Aseem ya qara Raina matsayin Asma'u tare da tsananin mamakin izzarta a matsayinta na wadda ta taso a wannan rubabbiyar unguwa a unguwar ma a gda mafi qasqanci domin shidai iyakar dubansa baiga gdan da yakai nasu Asma'u lalacewa ba a area.

Mal Husaini ne ya shiga ciki ya sanar da matansa cewa zaa shigo ganin gda me tankade ta tashi me dakama ta miqe sukayi daki Inna ce dama tana daki a zaune tana lazumi shigowa sukayi suna duba gdan a zahirin gdan Babu uwar da Aseem zaiyi dashi Amma  da suka gama dubawa sai ya dubi Zahran yace masa “ina ganin kamar gurin zaiyi ai ko?" Sarai Zahran yasan

me yake nufi shikuma sai yace “dadai an nemi Wanda yafi wannan gsky shanun zasu takura" dafashi yayi yace “kada ka damu fashe dakunan zaayi daki biyun nan kawai zaa bari saboda me gadi da abincin dabbobi" da wannan suka juya zasu fita suna Shirin fita kyawawan yammatan na sawo Kai Dijangala ce a gaba sai Zabba'u ita kuwa gwanar ta cake a qofar gda Laila sarkin soyayyya ita da Sadiqun ta suna bawa fure ruwa ai suna fitowa tana dago Kai suka hada ido ba itaba shima Saida yaji gabansa ya fadi ya kasa dauke ido daga kanta dake dariya takeyi yanzun sabanin duk haduwar da sukeyi dashi yau saiyaga tayi wani haske tayi kyau kyawawan haqoranta ya zubawa ido da akayi musu kwalliya da siririyar wushirya.
Ganin fitowarsu daga gdansu yasata saurin tsuke fuska kamar ba itace take dariya ba ta kawar dakai daga kallon da sukewa juna ita da Aseem din, sosai Sadiqu ya lura da sauyin nata don haka ya dubeta.

Yace “ya akayine jarumar Mata?" Ajiyar numfashi tayi tace “meye ya kawoshi gdanmu?" Da rashin fahimta yace “wafa?" Duban Aseem tayi da ya juya baya jikin motarsa yana waya tace “wancan Mara mutumcin Mana shine fah mutumin da nake baka Ibrn na fashewa qafa ko qarata ya kawo gda gurin Mal tab aikuwa zan daku shikuma zai ragargazu Dan wlh hayar tantiran hayin qwari zanyi su rugurgujeshi.
Dariya Sadiqu yakeyi Mata domin ya lura gabadayanta a tsorace take tsinkayo muryar Mal tayi Yana qwala Mata Kira “Ma'ulele ke Ma'u bakijina ne bakiga mutane ba dan qaniyarki irin tarbiyyar da gyatumarki tayi Miki kenan?" Sumsum ta nufi gurinsu duk a razane take a rusuna tace “ina yininku" Zahran ne da Mal Bala suka amsa shikuwa gogan kallonta kawai yakeyi Mal Bala yace “Mal nayi nayi dakai ka bani daya cikin yammatannan naka kaqi da tuni baba nakece maka ga Ma'u ma ta girma abinta" tsuke fuska Mal Husaini yayi yace “yo Banda abinka yaro ai sai yaro kaga wancan kafirin yaron da qaton Kai shine ya zamemin alaqaqai nayi nayi na rabasu sunqi rabuwa harma na hqr basa zanyi suje su qarata"
Dagowa Aseem yayi yace “wai itama wannan din taka ce Baba?" Murmushi yayi yana sosa qeya yace “wlh kagansu Nan kamar yar maraqan shanu haka akayita jeramin su harsu uku gasunan kansu daya ita wannan itace qaramarsu shekararta sha shidda sabodasu nema zan sayar da gdannan" Jinjina Kai yayi cikin jin dadi yana hango nasara yace “a aikuwa ba ayi haka ba kasai da gda baba kaida kake da Yaya Mata kabar gdanka kawai" da sauri ya dubeshi yace “inbar gda fah kace Alh waye zaiyimin auren yayan?" Murmushi Aseem yayi ya bude motarsa ya bude dashboard ya dauka raffers ta dari biyar biyar guda biyu ya bashi yace “karka damu baba ka riqe wannan gobe insha Allahu zan dawo ai kamarka kanada wadannan kyawawan yammatan ba abarka ka tozarta ba" sake miqa Masa wata reffer yayi yace a rabawa matan gdan wannan anan suka qyale Mal Husaini sake da baki da kudi a hannunsa suka dauki Mal Bala suka tafi a mota Aseem ya dubi Mal Bala yace “yarinyar nan data gaishemu ta fanshi mahaifinta indai zai bani auranta na rantse zanyi Masa komai da yake buqata na hidimar aurensu tun daga satin farko har ranar da zaa gama biki ka sameshi ka fada Masa idan ya amince har gdanma zan gyara Masa"..........
[20/06 4:27 pm] Oum Hairan: *ZARRAH*

_Tare da Alƙalamin_

*_Oum Hairan_*

_Bismillahir Rahamanir Rahim_

_Free Page 11-12_

*_Wattpad realfauzahtasiu_*

Telegram
👇
https://t.me/joinchat/Gdtmu0TgTHu66CF7

________________________________
________________________________

Tunda suka tafi sukabar Asma'u da sakakken baki kallon da Aseem yakeyi Mata ita da Sadiqu shine yafi Bata mamaki da Kuma dalilin zuwansu gdansu ganin ya damqawa Mal Husaini kudine yasata sake maida hankalinsu garesu amma sai taga ya dubeta yayi murmushi yaja motarsa sunbar Mal da kallon kudi cikin mamaki.
Mal Husaini na dagowa suka hada ido da Asma'u yayi saurin sanya kudin cikin hularsa tare da watsa Mata daquwa tayi saurin kawar dakai sukaci gaba da tsinkar furensu ita da Sadiqun ta Saida aka Kira magariba sukayi sallama ya nufi masallaci ita Kuma ta shiga gda ta dauki buta ta shige bayi ta Kama ruwa ta fito ta daura alwala daidai Ikcn da taji Mal Husaini na cewa “ni Babu ruwana da inda Zaki Amina gdane saidashi zanyi dole kowacce ta nemi inda zata zauna kafin ayi bikin yarannan ku koma qauye ba Saida nace kada ku kuskura ku haifi Mata ba ku masu kunne qashi kuka haifesu ai gashinan basu kawo kudi ba sun kwamushe muku naku" cafkar kunnen Asma'u yayi yace “ja'ira da kanta tunna zuwa duniya saura naji kince wani Abu baki kamar gdan tsutsa tana tafe kamar allura" itadai tana samu ya sakar Mata kunne sumsum ta shige daki ta tayar da sallah tare da jan bakinta ta tsuke Abu daya ta iya tambaya shine meye ya kawo baqin gdansu? Inna tace Mata. Masu siyan gdansu ne daga haka tayi shiru da bakinta saboda batason subutar baki tasa tayi wata magana don Bata kuskura ta fadawa Inna tsiyar da tayiwa Aseem Shaheed ba.

Kwana Asma tayi tana tunanin dalilin da yasa Aseem yakeson siyan gdansu, a daren taci alwashin indai Allah ya hadasu gobe a hanyar makaranta sai taci mutuncinsa yanda zaiji bama ya sha'awar siyan gdan nasu, aikuwa tun asuba ta shirya taja ta zauna tana jiran Ikc bakwai daidai ta fice daga gdansu ta nufi gdansu Jiddah suka dunguma suka tafi tana bawa jiddah labarin abinda ya faru jiya na zuwan Aseem gdansu a matsayin Wanda zaisai gdan zaiyi kiwon shanu"
Dariya sosai Jiddah tayi tace “kin gamu da qarfen qafa me wuyar kwancewa wato gayen nan ya shiryawa wasan so yake ya qure malejinki ya wulaqantaki Kinga idan ya siye gdanku ko haya ya baku ai babanku ya koma qarqashinsa balle ma tashinku zaiyi a wulaqance ya zuba shanu a gdan Kinga ya nuna Miki rayuwar shanunsa tafi taku muhimmanci. Nifa dama bangano Miki nasara a buga wasa da wannan mutumin ba da ganinsa kinsan yaci yatada Kai zai iya ramawa wulaqancin da zakiyi Masa ta duk inda yaso gara dai yan gujaru gujarun da muke tsokana Basu da yanda zasuyi damu sai tsaki sai harara"

Har sukaje makarantar Allah be hadasu dashi ba haka ta rinqa Allah Allah a tashi nanma Basu gamu ba taji haushi sosai so batada yanda zatayi dole ta hqr tana zuwa suka nufi islamiyya sai yamma suka dawo liqis dake laraba ce sunyi hadda a dakin zaure suka tarar da Mal Husaini da Mal Bala suna tattaunawa Mal Husaini sai dariya yakesu suka durqushe suka gaishesu da fara'a Mal Bala ya amsa inda Mal Husaini yace “Ina Ma'ulelena zonan dan qaniyarki" gabanta ya fadi tunda dama a tsorace take tana jiran abinda zaije ya dawo.
Matsawa tayi a darare ta zauna tana barin jiki don tasan ba wuya bane Mal ya maketa ba gyaran murya yayi yace “Ina kike Asma'ul Husnah?" Ajiyar zuciya tayi tace “gani Mal" Jinjina Kai yayi yace “yawwa Masha Allah dama wani umarnin gaggawa zan baki Kinga dai a yanda kuka taso a wahale a talauce to ke ki godewa Allah yasoki da arziqi yayi miki ludufi da ludufin da yakewa duk Wanda yaso cikin bayinsa jiya anzo ganin gida Ashe rabon aganki ne dan farin yaron nan Alhajin Birni eh wlh tallahi shine dai bayan sunga gda kinje kin gaishesu yagani yakeso harma yayimin alqawarin idan na bashi aurenki zai barmin gdana Kuma zaiyimin komai na auren Dijangala da Zabba'u keko yace ki cokali bashi buqata, kinji fah inda arziqi yake"

Tunda ya fara mgnr ta kafesa da ido cikin mugun tsoro da kaduwa ta gane waye yake nufi domin Zahran ba fari bane Aseem ne fari Anna sai tace “wa...waikace Mal Sadiqun fah?" Wata uwar harara ya buga Mata yace “Sadiqun0 ubanki yo ko Laminu ne uban Sadiqu ya dawo duniya ai bazai hanani cin wannan arziqin ba ke nifa bama shawara nake daku ba dagake har uwarki dama na dauka ke dake kin shafi zamani zakiba da hadin Kai to kema naga qwalluwar yar baqin ciki ce saboda haka tashi ware kauce karna makeki sauna kawai wadda arziqi ke binta tsiya ke dawo da ita baya"
Yana fadin haka ya miqe abinda yasata miqewa itama da gudu tayi cikin gdan tana rushewa da

kuka tana cewa “wlh baa isaba bazaa taba cutata a hadani da wannan shegen azzalumin mutumin ba ai bani kadai aka Haifa a gdanba abashi wata Mana saini saboda an rainamin hankali...." Jin takun sawayen Mal Husaini yasata shigewa qarqashin gadon qarfen Inna tana kuka ya shigo dakin yana huci Yana cewa “kajimin mutane yan baqin ciki arziqi yazomin har gda Allah ya amsa addu'a ta Nima nakusa hutawa shine zakuyimin baqin ciki tabdi ai wlh baku isaba wannan aure me hanashi saidai mutuwa idan ma mutuwa zakiyi saidai ki mutu ja'irar yarinya kina tafe kamar ki karye saboda rama yo kika sake kika auri Wannan Dan gadon talaucin da ubansa tunda nasanshi da tàgiya daya nasanshi basai kin qwammace wannan makauniyar uwar taki barinki tayi ba"

Harya gama sababinsa ya fita Inna batace komai ba sai bayan ya fitane Asma'u ta fito tanata shassheqar kuka Inna tace “wai waye wannan ne daga zuwa Mal ya aminta dashi Babu binkice Babu komi?" Nan Asma'u ta yiwa Inna bayani Inna ta saki salati da sallalami tare da yiwa Allah kirari tace “naga takaina ni aminatu dama akan wannan kwasasshen mutumin Mal yacimin mutunci har Yana cimin alwashin aure Babu fashi aikuwa da fashi don baza'ayi wannan son zuciyar dani ba yaro shekara da shekaru Yana wahala Rana tsaka saboda son abin duniya Mal ya rufe ido yana cima mutane mutumci ai bake kadai ya haifaba yabasa wata Amma bake ba"

Dayin magariba kuwa saiga Kiran Sadiqu a qofar gdansu idanun Ma'u sun kumbura sunyi luhu$^{2}$ saboda kuka ta yafa mayafinta ta fito shima duk a hargitse yake yana ganinta ya riqo hannunta yace “Asma'u meye ne ke Shirin faruwa dazu Baffana yayimin kiran gaggawa naje yake fadamin Wai saqone daga Mal babuni Babu ke yayi miki miji hakanne da gaske Ma'u rabani zaayi dake?"
Kafin ta gama shassheqarta ta dago sukaji daga bayansu muryar Mal Yana cewa “eh hakanne babu Wai a ciki nama rabaku har abada indai nine mahaifin Asma'u to babukai Babu ita nayi Mata miji daidai da ita kaima kaje ka samu daidai dakai dama ai a rashin uwa ake uwar daki tunda uwa tazo kuwa dole uwar daki ta kauce soko kawai me hatimin talauci a goshi"

A sanyaye Sadiqu ya tsugunna gaban Mal Husaini yace “Kada kayimin haka Mal wlh idan ka hanani Asma'u kamar ka datsemin farin cikin rayuwa ne ka taimakeni kabarni da Asma'u nayi maka alqawarin Bata farin ciki fiye da Wanda kake hango Mata a Wanda kake Shirin aura Mata Mal baisan darajarta ba kamar yanda na San...."
Tsawa Mal Husaini ya buga Masa yace “kajimin yaro sakarai Shashasha aiyo wato Nima kana

nufin kafini sanin darajar Asma'u ko to kaji in fada maka ba daraja ba ko alqabba ne Kai qarewar daraja Asma'u ba rabonka bace, kekuma munafuka na dawo kanki daga yau sai yau idan na qara ganinki da wannan faqirin yaron me riga daya saina Saba miki. Zaki shige gda kosai na karya qafafunki" a guje Asma'u ta fada gda tana kuka inda ta ishe Inna tana sallah fadawa tayi saman gadon qarfen Inna Mal Husaini ya biyota Yana cewa “wato Ni akeson a tozarta a garin nan a mayar dani sakaran uba da Bai Isa da gdansa ba ko to wlh baa isaba dole ne nasa doka abi ke Aminatu kin rainani Ina fada da babbar murya duk ranar dana qara ganin Ma'u da wani a Aseem ba sainaci mutuncinki wlh saikin gwammace baki sanni ba domin ranar ne zaki gane Nima namiji ne talauci ne yasani zama mace wawaye kawai masu qashin tsiya [20/06 4:30 pm] Oum Hairan: *_ZARRAH_*

*_Oum Hairan_*

*_13-14_*

Tunda Asmah ta taji wannan hadi da mahaifinta ya shirya yi mata ta shiga dimuwa da tashin hankali abubuwa suka jagule mata ta shiga tsananin damuwa abubuwa duk suka rikice mata ta kasa gane ta Inda aka samu asalin barakar sosai take cikin qunci,
A bangaren Dr Aseem Shaheed jinsa yake cikin walwala sabida ya samu yanda yakeso mahaifin Asma'u sai ladabi yakeyi masa shima kuwa ya sakar masa kudi tunda ya fahimci kwadayi ne dabi'arsa tuni yasa aka fara gyarawa Mal Husaini gidansa tunma kafin a gama daidaita tsakaninsa da yartasa.
Itakuwa Innah tsallle tayi ta dire tace bada itaba bazaa taba yaudarar Sadiqu da itaba yaron tun asmah batasan kanta ba yakeyi mata wahala sai yanzu rana a tsaka wani yazo a dauki aure a bashi wannan ai rashin adalci ne, sosai Asmah ta samu goyon baya gurin Innah hakan ya dan kwantar mata da hankali kadan.

Karatunta ta mayar da hankali tare da cin alwashin duk ranar da Dr Aseem ya kuskura yazo qofar gdansu saita tata masa asalin rashin mutunci, sati guda da zuwansu na farko tana kwance a dakin Innah abin duniya yayi mata zafi qarfi da yaji Yaya Mudam ya hana Sadiqu zuwa gurinta saidai su hadu dashi a burtsatse su tsaya suyi yar hirarsu babban tashin hankakinta yanda masoyin ya rame yayi duhu da sun hadu sai ya fara yimata magiyar karta yarda a rabasu a mafi yawan lokuta suna kuka suke rabuwa duk da cewa Asmah bata gama gasqata mgnr auren ba,
Hakanan aketa gyaran gdansu ita kuma tanaci gaba da zuwa makarantarta har tsayin watanni

biyu sosai rayuwa ta fara canzawa a gdansu mal Husaini har buhun shinkafa yake ajiyewa inda itakuma a haukanta ta fara mantawa da aikin dake tunkarota. Kwatsam ranar Wata alhamis sun dawo daga tahfiz ita da Jiddarh Jiddarh ta biyo zata karbi wani text book.

Tun daga nesa ta hangi wasu manyan motocin alfarma a qofar gdansu guda hudu hakanan gabanta ya yanke ya fadi suka kalli juna cikin sanyin jiki daidai lkcn da wasu fararen dattijai suke fitowa daga soron gdan nasu ta zubansu ido tanason ganesu amma ta kasa sai ajiyar zuciya kawai data suke ta rabasu ta wucce sudinma binta sukayi da kallo.
Itadai ko arziqin gaisuwa basu samu ba tayi shigewarta gdan garama Jiddarh ta gaishesu suka shiga tabata abinda zata bata ta fito ita kuma ta dauko buta ta fito, mamakine ya cikata ganin matan gdan nasu da yaransu Dijangala da Lantana a tsaye cirko cirko to dake ba shiri suka cika ba hakanan tayi shigewarta bandaki tanajinsu sunaja mata tsaki bata ko kallesu ba, fitowa tayi ta shige dakin Innah ta ishesu ita da mudam da Mal Husaini suna tattaunawa,
Kallonta mal Husaini yayi yace “nemi guri ki zauna duk na gama mgn da yan'uwanki kece kikeson ki bani matsala kuma ke dinma baki isaba"

A gajiye ta nemi guri ta zauna Yaya mudam ya zabga mata harara ta sunkuyar da kanta Mal yaci gaba da cewa “dazu iyayen Aseem sunzo akan batun aurenki sun kawo kudin aurensu da sadaki sannan sun nemi alfarmar ayi biki nan da Wata biyu dadai nace Wata biyar nasa so munyi mgn dashi Aseem din yacemin babu komi zai dauki nauyin komai wannan tasa da naga sauqi yazo na amince...."
Dagowa tayi da Sauri tace “Baffa Sadiqun fah...." Jitayi an buge mata baki ta dago da idanunta daya kawo ruwa take ta fara tsiyayar da hawaye Mudam ya nunata da yatsa yace “shegiya me qashin tsiya arziqi na kiranki tsiya na cewa nice taki ana mgnr arziqi kina mgnr talauci ubanme Sadiqu zaici bare ya baki gayyar tsiya gayyar wahala....."

Dagansa hannu Baffa yayi yace “yo miye na bata bakinka abuda babu fashi sai anyi kawai kije ki fara shiri nanda watanni biyu zan daura muku aure kowa ta kama gabanta" miqewa sukayi zasu fita cikin gunjin kuka Asmah tace “Innah bazakice komai ba don Allah kiyi wani abu...."
Janyota Innah tayi jikinta tana Shafa bayanta sukayi ficewarsu sannan ne Innah tasamu damar mgn tace “to me zance Ma'un Innah kinji irin diban albarkar da Mal yayimin yau har yana cewa nice nake zugaki kiqiyi masa biyayya, Asma'uh wannan lamari son zuciya ne saidai kawai Allah ya sakawa wanda aka zalumta kiyi hqr kiyi biyayya insha Allah zakiga Ribar hakan a gaba"
Kwantar da kanta tayi a jikin Innah tace “wlh Innah badon Allah Aseem yakeyin duk abinda yakeyi ba akwai manufa cikin lamarin nan Innah kada kibari son zuciyar su Baffa ya salwantar min da rayuwarta......"

Rufe  mata baki tayi tace “Asmah kiyi hqr kuma kisa  kyakkyawar niyya a ranki  insha Allah Ribar abin zaki gani" sosai Innah ta rinqa yima Asmah nasiha hardai ta daina kukan ta koma  ta kwanta  lamo akan gadon Innah tanajin zafin abinda Baffa yayi mata shi bayama  jiye mata wulaqanci?
Ranar ko diban ruwa kasa zuwa tayi saboda zazzabin da yake  damunta

Washegari juma'a duk da batajin dadin jikinta haka ta shirya ta fita domin zuwa makarantar daga  yanayin takunta Indai kasanta zakasan akwai  abinda yake damunta, cikin saa tana zuwa gdansu Jiddarh ta ishe  ta shirya suka nufi makarantar a qafa suka tafi  domin dukkansu babu mai kudin Mota suna tafe ne tafiya irinta kurame babu me cewa wani, sunci rabin  tafiyar sukaji Mota a bayansu tanayi musu horn basu  tsayaba saidai kaucewa da sukayi suka bawa mai motar  hanya, zartasu yayi sannan  ya tsaya tare da kashe motar ya fito cikin shigarsa ta likitoci fuskarsa dauke da murmushin da shi daya  yasan ma'anarsa ya tako  inda  taja  ta tsaya tana qare  masa kallo batayi aune ba kawai saiji tayi ya sanya  hannunsa ya dago fuskarta ya dora bakinsa saman kuncinta ya janye a hankali yana murmushi  yace “to ya kikaga salon wasan namu?"

Takaici ne yasa batasan sanda  wasu  hawaye masu  zafi suka zubo mata ba murmushin fuskarsa ya fadada yace “tun yanzu? Haba  karki karaya da wuri mana aike jaruma ce  kin iya rashin kunya zaki qwaci kanki dadin dadawa gashi kinyi saa  gyatumai kwadayayyu Allah ya baki kada  ki matsawa zuciyarki wajen tunanin abinda ya dace duk wani Abu da yake ya dace nayishi bayan iyaye shima masoyin na bogine  tunda ya siyarmin da soyayyar a farashi me arha dubu dari  da hamsin kacal kinga ko yanzu zaki iya  bambamce tazarar dake tsakaninmu koda yake banson  ma ki gane  yanzu ki bari sai can gaba saiki gane  lkcn da hakan zaibada show na gaske a lkcn ne wasan zai fara nanda 2 months yanzu sharar fage ce"..........

_Gareku yan'uwanmu na Niger kuma fah kuna  da damar  samun wannan littafan guda biyu idan kinaso kiyimin mgn ta WhatsApp akan wannan number,09013718241 sai najiku_

*_Oum Hairan_*
[20/06 4:32 pm] Oum Hairan: *_Zarrah_*

*_Fauziyya Tasiu Umar_*
*_Oum Hairan_*

Littafin _*_ZARRAH* na kudine idan kinason zaki biya 200 ta _account dina_ __0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTBank_ _ko kati MTN ta whattsAp a wannan number 09013718241 ko VTU ta wannan number 09031307566._

_Gareku yan'uwanmu na Niger kuma fah kuna da damar samun wannan littafan guda biyu idan kinaso kiyimin mgn ta WhatsApp akan wannan number,09013718241 sai najiku_

*_15-16_*

*_Last Free page_*

Sosai hawaye kibin kuncinta tana qara saita injin idonta akan Aseem kallo takeyi masa da yake bayyana tsantsar tsana dajin haushi da kuma tausayin kai tasan duk duniya ba kowane yaja mata wannan wulaqancin ba face Mal, numfashi ta sauke kawai ganin wankin hula na neman kaita dare ta juya ta canza hanya ta tafi tabarsa tsaye yana bin bayanta da kallo yana murmushin mugunta shikadai tasan abinda yake saqawa a zuciyarsa yarinyar ta gama lalacewa idan ta zama mallakinsa zai nuna mata iyakarta zai nuna mata duniya da bambamci.
Komawa yayi yatada motarsa ya tafi sai lkcn Jiddarh ta lura da cewa ashe Asmah ta jima dayi mata nisa tabita da sauri tana qwala mata kira bata tsaya ta saurareta ba sai a cikin makaranta suka hadu bayan an gama assembly suka tafi ajinsu Jiddarh ta dubi asmah tace “wato Allah idan yana sonka da arziqi sai ka zagi sarki a gaban fadawa yace gaisheshi kayi wlh Asmah a rayuwata na dade banga kyakkyawan namiji irin Aseem Ba kayy gsky kin dace, amma fah da alamun dan izzar masifa ne zakisha fama...."

Wani naushi da Asmah ta kaiwa Jiddarh a baki yasata gocewa tare da cewa “daga fadar gsky kuma Allah mijinki dan kyakkyawa dashi" malaminsu ne ya shigo hakan ya tilastawa Jiddah yin shiru ita dama Asmah bakinta ya kulle kalaman Aseem ne kawai sukeyi mata yawo a kwanya iyayenta matsiyata idan ta tuna wannan kalmar sai taji hawaye ya zubo mata to amma komai ya

samu shamuwa watan bakwai yaja mata da mahaifinta baibi son zuciya ba da yanzu tana tare da masoyinta,  da taji haka a ranta saita tuna yace da quarter million ya siye Sadiqunta. Gabadaya duniya tayi mata zafi ji takeyi kamar tayita rusa kuka hakadai a dafe aka tashi suka tafi gda daqyar takai gidan saboda azabar masifar zazzabi da yake dirar mata tana zuwa ko uniform bata cire ba ta fara kwara amai bayan ta gama ta shige dakin innah ta kwanta tana mayar da numfashi

A kwance take amma duniyar juya mata takeyi itadai bata qara sanin komai da yake faruwa ba sai farkawa tayi ta ganta daure da robar ruwa a hannunta ta rinqa bin dakin da kallo daya da daya tanason tunano ko a ina take a hakan taji an turo qofar an shigo ta juyo da kanta idanunsa na kanta yana wani lumshesu kamar me jin bacci.
Guri ya samu ya zauna ya bude takardar hannunsa yayi rubuce rubucensa ya rufe ya sake dagowa yanzun kanta yana saman silling fasali yaja ya miqe daidai lkcn da Inna Azeezah qanwar Innah take shigowa suka gaisa har yana wani rusunawa tace “ya me jikin?" Kallon Asmah yayi yace “gatanan da sauqi yanzu ta farka da alamun jikin dakyau insha Allahu gobe ma zamu koma gida  yasu Innah?"

“Alhmdllh" ta furta koma ta zauna tana hade kaya shikuma ya fice bai jima ba ya dawo da tarkacen ciye ciye ya ajiye Innah Azeeza nata godiya  yayi murmushi  yace “babu komai Innah yiwa kaine fatanmu dai ta samu Ify ai taji jiki sati biyu a kwance ga hidimar biki sai matsowa takeyi yanzu fah saura sati biyar" jinjina kai tayi tace “Allah yasadai ayi Ify a gama Ify"

Amsawa yayi da amin sannan yasa kai ya fice  zuciyarsa najin haske yanajin nishadi yasan yagama saita saarsa Asmah zata gane kurenta tabbas zatasan ta shigo gonarsa da wannan tunanin ya tashi mota ya nufi gdansa yajima a mota kafin yayi qarfin halin fitowa yana ayyana ta yanda zai tunkari Mime da mgnr auren nasa bayan shi da kansa yayi mata alqawarin bazai taba hada matsayinta da wata ba balle aje ga batun aure.
Shahada yayi daya haura ya tunkari saman a kwance a parlourn saman ya isheta tana duba jarida ya nemi guri ya zauna ta ajiye jaridar tare da dagowa ta dubeshi sukayiwa juna murmushi ya shafa kansa yace “ya gda?" Miqewa tayi zaune tana yatsina tace “gashinan babu dadi kadaici ya dameni kaikuma ka daina samun lkc na na rasa meye yake daukenka hankali gareni" kawar dakai yayi ya shafa sumarsa yace “abubuwa ne sukayimin yawa 2 days dinnan inason samun zama dakema nakasa samun lkc” shiru tadan ratsa na dogon lkc can ya dago yace “Maryam Aure zanyi....." Wata zabura tayi ta miqe da sauri tace “me....me kace Aseem".......

[20/06 4:32 pm] Oum Hairan: *_Zarrah_*

*_Fauziyya Tasiu Umar_*
*_Oum Hairan_*

Littafin _*_ZARRAH* na kudine idan kinason zaki biya 200 ta _account dina_ __0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTBank_ _ko kati MTN ta whattsAp a wannan number 09013718241 ko VTU ta wannan number 09031307566._

_Gareku yan'uwanmu na Niger kuma fah kuna da damar samun wannan littafan guda biyu idan kinaso kiyimin mgn ta WhatsApp akan wannan number,09013718241 sai najiku_

*_17-18_*

Miqewa yayi yana shirin shiga daki ta riqoshi ta baya tace “wai da gaske kunne na yakeyi kaine kake fadawa Mimee zakayi aure Aseem da gaske hakane? Please tabbatar min domin nasan tudun dafawa" kama hannunta yayi ya zaunar da ita yana binta da kallo yace “ba kamar yanda kowanne aure yakw nawa yake ba Mimee idan kika tashi hankalinki ke kikaga dama da kanki zan Aure ne domin ramuwa da daukar fansa, idan baki manta ba nataba baki Ibrn wata yarinya data mareni ta fasamin yatsa kwanakin baya, to itane zan aura, a zahirinta ba ajina bace kuma ba tsarata bace ni kaina inajin kunyar hadaka ta da ita ina qyaqqyaminta wlh don an daina cinikin bayi ne da siyo miki ita zanyi matsayin baiwa ki rinqa morarta

Dakatar dashi tayi da sauri tace “shut up Aseem banason yaudara da zalimci ni zaka wulaqanta ashe dsma abinda ake fadamin gsky ne Wayyoh Aseem meye nayi maka da zakayimin wannan sakayyar...." Rufenta baki yayi yana girgiza mata kai yace “kada ki kawo komai a ranki ba haka nake nufi ba har abada kece zabina kece burina kuma kece zuciyata wlh da gaske yarinyar nan don ke na aurota nasan zata taimaka miki

Sake dagansa hannu tayi ta miqe da gudu ta nufi dakinta ya bita da sauri  daqyar ya samu ya shawo kanta bayan yayi mata manyan alqawura masu  wuyar cikawa yana qara rantse mata baso bane zaisa ya auri Asmah kawai gayya ce to ganin yanda ya zage yana rarrashinta yasata sakin jiki amma duk da haka kishin mijinta yana cinta a ranta duk da tayi ammannar bai isa ya wulaqantata ba kodon soyayyar da mahaifiyarsa takeyi mata dole yabi umarnin uwarsa saboda haka ta yanke shawarar binsa ta qasa zata hadashi da hajiyansa tasanta sarai bata hada hanya da takala balle  kuma ta bari a kawo mata yar  matsiyatan qarshen zamani matsayin suruka da wannan tunanin suka fita ko a hanya aikin rarrashin mimee yakeyi suna shiga harabar gidan yaji gabansa yana faduwa so yayi ya juya amma INA ya makara yana daga Kansa ya hango hajiyansa saman bene ta zubawa motarsa ido dole tasashi fita yabi bayan Mimee data shige gdan a qofar falon sukayi karo da Hajja ta daukeshi da mari ya dafe  gurin  da tafukan hannunsa yanajin zugin marin  saman jar fatarsa yana dagowa ta sake daukeshi da mari tana kumfar bakin  cewa yanzu Aseem har kayi qwarin da zaka nemi aure  batare da ka sanar dani ba saidai naji a wajen qannenka....."
Hawaye Mimee ta goge tace “ai dole bazai fada miki  ba Hajja wai  ya rasa dawa zai hadani kishi saida yar  talakawa...." Dafe qirji  Hajja tayi tace “na shiga uku ni  Saratu yar  talakawa Aseem ina  ka samota me suka Baka suka sauya maka tunani  ni  zaka wulaqanta yanzu yaushe ma akayi aurenka da Maryam da har zaka tattagowa kanka aure  kuma auren ma memakon kaci gaba sai kawai kaci baya to wallahi baka  isaba dole ka hqr da wannan dan iskan auren naka  ka zauna da matarka dana  zaba maka"

Shidai  tunda yayi qasa da Kansa bai dagoba sai yanzun yace “wlh Hajja ba haka bane kawai...." Buge masa baki tayi tace kawai Ubanka ka kiyayeni Aseem zanci ubanka wlh dama na lura shine yake  daure maka gindi  shi ko ubanme ya hanashi auren mace sama da dayan sai kai da quruciyarka zaka dorawa kanka wahala to indai na isa  dole ka janye ban amince ba bakuma zan amince ba"
Juyawa tayi  ta shige parlournta ta barshi tsaye itama Mimee tabi bayanta a sanyaye ya juya ya fice daga gdan yanajin zafin abinda Hajja tayi masa yanzu meye laifinsa don anyi masa ba daidai ba yayi shirin daukar fansa  zaayi masa wata  fassara ta dabam bandama  abinsu shi meye zaici da wannan banzar yarinyar da bata isheshi kallo ba"

Da wannan tunanin ya nufi gdan Jabir yake  fada masa abinda ke faruwa sosai shima Jabir ya jinjina abin ya dubesa yace “to kai tunda abin baiyi nisa ba ka hqr mana kasan dai  halin Hajja shi kansa  Dad hqr yakeyi da ita" girgiza kai yayi yayi murmushi yace “nifa babu abinda zaisa na

janye akan qudurina saidai kowa yayi hqr kamar  yanda nake  haqurqurtar da zuciyata ta karbi auren idan na janye dama  haka Asma'uh da nahaifiyarta sukeso farin ciki  zasuyi nikuma ba burina  suyi farin  cikin ba saboda haka kawai aci gaba da tafiya a haka tunda Dad ya karba mgnr kowa ma kada  ya karba" da wannan tunanin ya miqe ya nufi gdan Yayarsa Aseemah itace kadai me sauqin yanayi a wajenta yake  tunanin samun mafita game da auren nasa yana zuwa ta tareshi da fara'a tana tsokanarsa nan yake  zube mata abinda yake  ransa sosai tayi murna ta tayashi fatan alkhairi yayi shiru kamar  bazaice komai ba sannan ya dago yace.
“Banasonta Sister na rasa meye yasa na dage  wajen Neman auren ta yar  talakawa ce  Allah ina  qyaqqyamin kaina inajin kunyar nunata matsayin mata talauci yayi musu kanta nifa badon quduruna a kanta ba da tuni na hqr ko na samu nutsuwa"

Zubansa ido Aunty Aseemah tayi har saida  ya rufe  baki tayi ajiyar zuciya tare da murmushi tausayin Asmah yafi komai narkar da zuciyarsa duk da tasan cewa qarya Aseem yake  yace bayasonta domin tasan zuciyarsa idan babu burbushin son babu abinda zai darsa masa son auren ta matsalar kafin ya aminta ya yarda  yanasonta tasha wahala kawar dakai tayi tace “kaje kayita addu'a qila rabone tsakaninku kasan  ba kowa ne yake da Baiwar gane  abinda yakeso a qaramin lkc ba" sosai ta rinqa basa  shawara wata  yakan dauka wata  kuma ya watsar da ita domin yasan bazai iyaba"
Baibar gdan ba sai bayan magrib ya nufi gdansa har lkcn Mimee bata dawo ba dakinsa ya shiga yayi wanka  ya dawo ya kwanta  a parlour ya kunna kallo.

**********

Tunda suka koma  gda  batada aiki  sai tunani  damuwa taqi damunta babban abinda yafi damunta shine yanda Sadiq ya manta da ita ko a hanya suka hadu sai ya kawar mata dakai koma ya buleta da qurar sabon lifan dinsa wannan Abu nayi mata ciwo gashi batada Wanda zata zauna tayi hira dashi taji dadi duk da zuwa yanzu sun daidaita da yan'uwanta so ta lura suma  yan son zuciya ne har garama Dijangala ita ta fahimci akwai matsala tana tausayawa Asmah sosai musammam da taga kowa saurayinta yana zuwa gurinta suyi hira itakam Asmah Aseem tun  ranar da aka sallamosu daga asibiti bai qara takowa gdansu ba saidai ya aiko Jabir duk ta rame  abinka da mara  jikin dama babu abinda kake  gani sai dogon hancin da idanu duk rawar kannan  da fitsarar  Asmah tayi laqwas ko mgn wahala takeyi mata ana haka aka kawo lefen su Dija samarinsu sunyi qoqari sosai babu laifi a matsayinsu na talakawa kwana biyu tsakani aka kawo na Asmah ranar har wanda  basa  mgn dasu saida  suka shigo ganin wannan lefe na al'ajabi

Lkcn bikin saura sati guda amma shiga shagalin biki itadai Asmah tunda aka fara bikin tana kwance a dakin da akayi musu na yaran gda batada aikin daya wucce kuka duk da fitsararta tasan haqqin Miji akan mace sosai yanzu indai ta bari aka daura auren nan shikenan ta zama nama duk yanda yaga dama haka zaiyi da ita? Hakan ba qaramin karyar mata da zuciya take ba ana saura kwana biyar tana gdan maqotansu tana kwance kasancewar ba Lfy ce ta isheta ba yaro ya shigo yace “wai ana kiran Asma'uh a waje" ajiyar zuciya tayi ta gyara kwanciya Jiddarh tace “ki tashi kije mana kinsan shima wannan dan Aiken ba qaunar jira yakeyi ba" Tsaki tayi tace “kije kawai" sanin halinta ne yasata miqewa tace “bazakiyi mana buqulu ba yanzu haka kudin partyn aka kawo mana" Dija nayi mata dariya ta fice itadai bata tanka ba sai game da takeyi da wayar Hajar Matar gdan da suke yammatancinsu, da sauri sukaga Jiddarh ta nufo parlourn ta zauna tana Mayar da numfashi saida ta gama saita nutsuwarta tace “aikin babba ne Ma'uh yau me gayya me aiki ne yake tafe wlh yanacan saici mazu yakeyi kije yana jiranki" sosai taji qirjinta ya buga ta dago idanunta da suka kawo ruwa tace “don Allah kije kice masa bananan" zare ido tayi tace “ban isaba wlh ki tashi kawai kije" sharewa tayi ta koma tayi kwanciyarta daqyar tasheta shima saida Innah ta aiko da kanta sannan ta tashi tasa qaton hijjab dinta ta fito idanunta na fitar da ruwa ta nufi wajen ta jima tsaye kafin ya danna mata horn ta nufi inda motar take ya bude mata kamar taqi shiga sai kuma ta tuna maganganun Innah haka ta zauna ya mayar da qofarsa ya rufe ya juyo ya zuba mata ido tayi qasa da kanta tana wasa da yatsanta hawayenta na zuva saman santala santalan yatsunta,

Sun jima A haka kafin taji yaja Wata doguwar ajiyar zuciya ya furzar da iska yace “meye yayi saura?" Jan numfashi tayi me hade da majina kukan da take ta qoqarin hadiyewa ya qwace mata yayi saurin zubanta ido tare da kamo hannunta qirjinsa na bugawa da qarfi kukan yana masa kuda a kunne yace “ya....ya salam meye kuma na kukan?" Sake rushewa tayi da kuka gabadaya ya diririce baisan sanda ya hadata da jikinsa ba ya rungumeta sosai ta rintse idonta da qarfi ta sake qarawa kukanta sauti tace “nas....shiga ukuna wayyoh Innata ka sakeni don Allah banas....." Numfashinta taji yana qoqarin daukewa ta shidewa tayi saurin bude idonta tsoronta ya nunku jikinta ya dauki rawa tunda take bata taba ganin dan iskan bayyane irin Aseem ba Shikam babu abinda yakeyi sai tsotsar lips dinta daqyar ta hada qarfinta ta tureshi tana jan zuciya tare da sanya hijjab dinta ta rinqa dirzar bakinta tana kuka me taba zuciya tace “Allah ya isana mugu kwarto kawai......"

*_Oum Hairan_*

[20/06 4:32 pm] Oum Hairan: *_Zarrah_*

*_Fauziyya Tasiu Umar_*
*_Oum Hairan_*

_*19-20*_

Buda idanunsa yayi akanta  yana mata wani kallo daya sanyata saukar da kanta qasa ta kama handle din motar zata bude yayi mata key ya tasheta ta dago da sauri ta kalleshi idanunsa nakan  tuqin da yake amma hankalinsa na kanta cikin sanyin muryarta ta kuka tace “Ina zaka kaini?" Bai kulata ba kuma bai daina  tuqin ba har saida  suka isa  wani gurin kwalliya ya bude motar  ya fita bai jima ba ya fito ya bude mata yanayi mata kallon dake firgitata ta fito a sanyaye yayi gaba tana binsa a baya har suka shiga ciki ya samu guri ya zauna tana tsaye yana qare mata kallo har saida  daya cikin ma'aikatan gurin tace “yallabai meye ake buqata?" Numfashi ya sauke ya nuna  Asmah dake tsaye kamar dashe tanabin gurin da kallo ya yatsina fuska yace “wai Amarya ce wannan din so jibi zaa  fara bikin zasuzo su biyar ayi  musu kwalliya nawa  ne zai isa?"
Nan sukayi masa bell ya biyasu ta shiga wani daki  tace ta biyota sharewa  tayi kamar  bazata ba ta tsinkayo muryarsa ya daka  mata tsawa jikinta na tsuma tabi bayanta suka shiga ciki kanta ta bude gashinta dake nade  cikin dankwalin ya baje Matar tace “masha Allah Amarya angonki zai huta da gashi" itadai bata saurareta ba saima tagomashin harara data samu ta wucce ta dauko  mata wasu  turaruka ta bata tace “gashinan dukkanku Ku rinqa wanka  dasu qamshi zai kama jikinku gobe kuzo da wuri ayi  tsifa jibi ayi  gyaran gashi jikinki zai dauki gyara sosai inajin gobe  zamu fara"

Bata qarasa jin abinda take cewa ba tayi ficewarta, ganin fitowar natane yasa shi miqewa ya biyo bayanta ta tsaya jikin  motar  yana zuwa ya bude

 Ya Shiga itama ta shiga yaja  suka tafi sunyi nisa sosai ya magantu da cewa r“anar Friday akwai dinner da dare ki zama ready" shiru ce  ta bashi amsa takaici ya cikashi a duniya yana baqin cikin yayi mgn a shareshi qwafa yayi dole ya gogewa yarinyar raini ya fahimci ta gama

rainashi tun yanzun parking yayi a qofar gdan kafin ya gama tsayawa harta fice tabar masa ledar turarukan da aka basu ta shige gdan Hajar.
Qarin takaici ya cikashi ya cije lebe a fili yace meye take taqama dashi ne?" Bashi da me bashi amsa dole ya kira wani Yaro yabashi ledar turarukan da Wata qatuwar Leda da shi Kansa baisan meye a cikin ba Aunty Aseemah CE ta bashi tace yakaiwa Asmah juyawa yayi ya tafi zuciyarsa cunkushe da takaici koda ya shiga gda bai nemi Mimee ba itama bata nemeshi ba ya shige dakinsa ya kwanta ya rasa meye yasa idan Asmah tayi masa wulaqanci abin yake kasa gogewa a ransa a hankali yaja qwafa ya miqe ya watsa ruwa ya dauki wayarsa ya hau online kusan sati biyu kenan daya bata waya baitaba ganin ta a bude ba sai yau tunda ya hau ya bude kyakkyawan hotonta da tayi tana murmushi ido hakanan yake jin gabadaya lakar jikinsa na tsinkewa tunda yake da ita baitaba zubanta ido ya qurewa kyawunta kallo ba sai yau tabbas Allah yayi halitta a gurin shiyasa take shuka tsiyarta son ranta.

Agogo ya duba yaga goma harda kwata yaja fasali so yake yayi mata mgn amma ya rasa me zaice mata ya jima yana tunanin me zaici kafin dabara ta fado masa ya rubuta mata _“ki sauka haka dare yayi"_ iyakar abinda ya rubuta kenan bayan kamar minti uku ta duba batare data bashi amsa ba ta kashe datarta ta sauka hakanma baiyi masa ba yaso ace tayi mgn

Hakan bata samu ba ya lura yarinyar yar izza ce ta bala'i dole sai yayi shiri me kyau domin zama da ita sai an shirya, tsaki yayi kawai ya gyara kwanciyarsa washegari da wuri ya tashi ya fice saboda yanada abubuwan yi da yawa kuma yanaso a gama aikin bangaren da zata zauna a yau gashi dai yau yake son ya turawa da Mal Husaini kayan dakin su Dijah, ya manta da batun zuwansu gurin gyaran jiki sai wajen 1:30pm aka kirashi daga gurin ake fada masa mutum uku sunzo amma wacce sukazo tare jiya bata biyosu ba,
Takaici ya cikashi ya dauki wayarsa a fusace ya lalubo number ta ya danna kira yajita a kashe baqin ciki ya hadashi sosai ya miqe tsam daga inda yake zaune ya figi motarsa a guje ya nufi unguwar cikin saa kuwa ya tarar da mal Husaini a qofar gda suka gaisa nan yace ya shiga dakin zaure bari ya kira masa ita, da Kansa ya shiga ya fara qwalanta kira tanaji gabanta ya fadi don tasan bana Lfy bane ta fito a salube ya harareta yace “yar baqin ciki to kije Alh nason ganinki" kamar tace masa Mal bazani ba amma batada iko hakanan ta dauki mayafinta tasa ta dauki wayarta dake saman window ta fita.

Ta jima a zauren tabarshi tsaye sai faman duba Agogo yakeyi kafin tayi qarfin halin buda labulen tare dayin yar siririyar sallama itama saboda ta zama dole ne, ba kwalliya ce a fuskarta ba hakan ya matuqar burgeshi tunda yake da Asmah baitaba ganin ta da kwalliya ba. Ya

shagala da kallonta kusan 15 minutes itakuma ta qosa da kallon ta dubesa a kaikace tace “zan iya tafiya?" Yanda tayi mgnr da muryarta me kama da me shirin yin kuka yasa shi zama a kusa da ita da Sauri wani gumi ya karyo masa ta goshi itakuma jin baida niyyar mgn yasata miqewa ta saita hanya zata fice yayi azamar riqo hannunta ba shidinba hatta ita saida taji wani shocking a gabbanta ta dago idonsu ya gauraya da juna sai wani lumshe fararen idanunsa yakeyi yana bude su akanta.
Hakan yasata qoqarin janye hannunta daga nasa maimakon hakan kawai saijinta tayi zaune a saman cinyarsa gabanta yabada wani rass abinka da matsoraciya gabadaya lkc guda ta hargitse shikam gogan qara gyara zamansa yayi hakan da yayi yasamu yanda yakeso manyan faffadan mazaunanta masu tudu suka danne masa burarsa da take ta qoqarin miqewa taimako daya Allah yayi masa yasa boxes daya kamashi kota miqe bazata nuna shi ba saidai yaji a jikinsa, sake sanya hannunsa yayi ya harde qugunta ya sanya su saitin Cikinta ya dora kansa saman kafadarta yana sauke mata wani huci me dumi da dumama yanayi.

Cikin dabara ta rinqa qoqarin zame jikinta yaqi bata dama har saida yaji ta soma shassheqar kuka sannan ya fahimci abinda yake shirin aikatawa ya sake ta ta zame a hankali ya kwanta saman kujerar three sitter din da yake kai tare da harde qafafunsa yana qoqarin aro kwarjini yasawa Kansa yace “meye ya hanaki zuwa gdan kwalliyar dana kaiki jiya?" Sunkuyar da kanta tayi har yanzu qirjinta lugude yakeyi itakam ta hadu da masifa wannan mutumin wanne irine me yake nufi da ita wanne salone wannan yake son zuwar mata dashi da yake Neman zarta girman kwanyarta a mizanin hankali.......
Ji tayi hannunsa na yawo a fuskarta ta dago da Sauri sukayi ido hudu yasa yatsansa

wasa da ruwan hawayenta yayi murmushin da yasa kuncinsa lomawa sajensa ya hadu da gumi ya kwanta luf a fuskarsa yace “Asma'uh Ma'un Innah Mara kunya fitsararriya wacce bata barin kowa idan tsautsayi yasa ya shiga gonarta am don Allah ki daina kuka kuka bai kamaci fuskar jaruma kamarki wacce ta shiryawa fito na fito da mutum kamata ba ki jira lkcn kuka na gaba lkcn da zaki gane shayi baikai matsayin ruwa ba domin shi ruwa haka ake buqatarsa shayi ko sai ansa masa Lipton da suger yake shawuwa, Kalmomin qarshe da nakeson sanar dake banson jayayya akan abinda yake hurumi na dole ne idan nasaki Abu kiyishi ko bakyaso kina nunamin jin dadinki kuma komai wahalarsa idan kin gama kiyimin godiya sannan koda wasa kada ki qara kashemin waya na kira ban sameki ba saboda banson shigowa wannan lungun talakawan dole ce take biyo dani am akwai sauran dokoki da sharruda na zama dani a matsayinki na baiwa don baki isa nayi miki kallon mata ba ke kanki kin sani zan baki jadawalin ayyukanki ranar da kika tare a gdana"
Shiru ce ta ratsa ta tsayin lkc har yanzu hawayen bai daina zuba a idonta ba yayi ajiyar zuciya ganin yanda ta lumshe manyan idanunta gashin idonta ya sauka saman kuncinta abin ya bashi nishadi bude bakinsa a saitin kunnenta yace “wannan dogon surutun ma da kika sani kiyimin gdy"

*_Oum Hairan_*
[20/06 4:32 pm] Oum Hairan: _*Zarrah*_

_*Oum Hairan*_

_*21-22*_

Sake qoqarin shigar  da ita yakeyi jikinsa ta sunkuya  a hankali tanajin quncin abinda yakeyi mata A ranta tace “don Allah ka kyaleni na tafi jirana akayi...." Sunkuyawa yayi ya dora hannunsa a bakinta yace “da hakan ma ni  meye yasa da nabaki umarnin kije kikaqi zuwa?" Yana mgnr yana dagota ta sake lumshe idonta yayi murmushi yace “ke jaruma ce  kuma mara kunya tabbas saurin kuka bai kamaceki ba" Yana fadin haka ya juya ya fice yana cewa dole kibi abinda na gindaya miki  idan kinqi kuma ki sake shigar da kanki  sawarwarin wahala sakarya kawai"
Bayan tafiyarsa ta jima tsugune a gurin kafin ta tashi ta fice daga gdan ta nufi gdan hajar tana zuwa ta kwanta kanta yana juya mata abubuwan da suka faru suna dawo mata nan Hajar tazo ta sameta tana tambayarta meye yake faruwa ta miqe zaune tare da jan fasali tace “wai zai aureni ne matsayin baiwa Aunty Hajar wacce irin bauta ke a cikin aure bayan wacce duk wata mace takeyi a gdanta?" Shiru hajar tayi tana nazarin kalamin kafin tace “to Allah shi dai yasan karatun Kurma kedai kamar yanda Innah taketa fada miki kiyi hqr kuma kiyi biyayya Allah bazai barki banza ba zai kawo miki dauki a dukkannin lamuranki yanzun meye ya kawoshi?"

Goge hawayenta tayi tace “akan banje gyaran jiki bane" harararta hajar tayi tace “ai dama saida aka fada miki baki gaji da zubar da hawaye bane shiyasa kikeqin daukar shawara kije kiyi abinda kikaga ya dace dake namiji ya aureka ma don qauna yaka qare bare wannan da ya aureki don gayya kada ki saita zamanki kije kina raba hali kishiyarki ta fahimci baraka tsakaninki da mijinki kigani in zakikai labari"
Sosai kalaman hajar ya kashe mata jiki tabbas wannan way din data dauka ba mafita bace gareta miqewa tayi ta zari hijjab dinta ta fice ta hau napep ta nufi gurin kwalliyar cikin saa taje angamawa kowa kawai aka hau yimata abinka da fata me kyau itan tafi kowa daukan kyau, hakanan bayan an gama suka tafi sai zuba qamshi sukeyi suna zuwa suka tarar ankawo kayan Dijangala da Rabi kayan sun gaji da haduwa kowa sai kodawa yakeyi.

Ko kallo basu isheta ba tayi shigewarta ta kwanta washegari aka shiga hidimar biki gadan² kowa yanata warkajami banda ita domin kuwa kowa daina kulawa tayi batada abokin hira sai wayarta itanma da taga zaa dameta take watsarwa tayi kwanciyarta a ranar ma saida sukakai ruwa rana kana ta yarda sukaje lalle da gyaran gashi yamma liss suka dawo juma'ah da safe aka kawo mata kayan dinner a wata qaramar akwati kayan sunyi kyau matuqa da yamma Aunty Aseemah ta turo aka dauketa bayan kwalliyar da sukaje akayi musu ta kuma gyarata tasa akayi mata shiri na musamman domin ita a ranta yanzun takejin qaninta yana aure domin wancan auren zabin mahaifiyarsu ne wannan kam duk da yana iqirarin bayaso tasan zabinsa ne. Daganan aka daukesu qarfe Shidda sai gurin dinner din ashe shima gurin dinner din uku ya kama nasu shine na musamman tare kuma a lkc daya motansu ya tsaya aka bude masa ya fito itanma aka bude mata ta fito suka hade a tsakiya sauti me dadi yana tashi itadai banda hawaye babu abinda takeyi tasan daga gobe shikenan kashinta ya bushe a hannunsa, tana tafe tana layi har suka isa mazauni anan akayi kamu da duk wata bidi'a sannan aka fara gabatar da dinner din suna zaune zaman kurame babu me cewa wani qala tsakaninsu wayarsa tayi ring ya zaro a aljihunsa ya kara a kunnensa bataji abinda akace ba tadaiji yace “ok ganinan"

Miqewa yayi ya dubeta kamar zaiyi mgn kamar wanda ya tuna wani abu yayi gaba abinsa tabi bayansa da kallo take MC din ya fara babatun “toh amarya ya haka kika bari ango ya fice wasa bai qare ba?" Wasu hawayen baqin ciki suka zubo mata ta miqe itama da sauri ta nufi hanyar fita da sauri Jabir ya riqota yana girgiza mata kai ta watsa masa wani kallo da yasashi sakinta yace.
“Kiyi hqr kiran gaggawa ya samu a asibiti shiyasa" bata saurareshi ba ta hankadeshi ta fice wannan abu yabawa kowa haushi a gurin da mamaki kowa nata fadin albarkacin bakinsa itakam tana fita ta tsari napep ta fada masa inda zai kaita tana zuwa gda ta fada dakin Inna ta zube a jikinta ta rushe da kuka sosai hankalin Innah ya tashi daqyar ta samu tayi shiru ta lallabata ta fada mata meye ya faru, murmushi Inna tayi tace “banda abinki Ma'uh Ify ai tafi komai kada kisa wannan a ranki komai zakiyi kiduba girman Allah ki zauna da mijinki Ify ki fahimceshi kinji" sake kwanciya tayi jikin Inna tana sauke ajiyar zuciya tace “Innah wlh inajin tsoron mutumin nan bashida tausayi kuma ni nasan ba domin allah ya nacewa aurena ba"

Ajiyar zuciya Innah tayi taja bakinta ta tsuke tanaci gaba da shafa bayan Asmah, a haka bacci ya dauketa lkcn goma ta wucce daqyar Innah ta gyaranta kwanciya da taimakon Innah Azeezah a daren Jabir yake fada masa abinda ya faru baiji haushin kansa ba sai ita yayita kiran wayarta tasata a silent ya kira yakai sau uku bata dagaba dole ya hqr amma rainin yarinyar yanacin zuciyarsa ranar kwana yayi yana huci Mimee na kallonsa bata kulashi ba don ta fahimci a yan kwanakin bashi da fushin daya wucce Asmah sai wajen biyun dare sannan ya kwanta shima

kiran wayar bai daina ba cikin saa kuwa ta daga cikin mayen bacci bai bari tayi mgn ba yace. “Ke wacce irin mara tarbiyya ce da zaki jizgani a cikin abokaina kinsan su waye a gurin kuma kinsan dalilin da yasa na tashi nabar gurin  ne shashasha sakarya mara tarbiyya....." Qit yaji ta kashe wayar ya miqe zaune da sauri yana kiran wayar yajita a kashe gabadaya yaja wani huci tare da cilli da wayar ya miqe kamar wanda aka tsikara ya zari mukulli sai kuma ya kalli agogo yaga uku saura wata ajiyar zuciya ya sauke ya koma ya zauna yana dafe kai yana mayar da numfashi  a fili yace “saura 7 hours zakiyi bayani duk wani iskanci da kike ji dashi zaki saukeshi a gidan matsiyatan iyayenki" Komawa yayi ya kwanta

Tunda ta farka taga kiransa ta kasa sake rintsawa wai yar marasa tarbiyya ta jinjina kalmar nan tafi sau hamsin kafin ta sake kwanciya wannan wanne irin miji Allah ya zaba mata da wannan tunanin ta tashi kawai tayo alwala ta tayar da sallah ta jima tana roqon Allah ya cire mata jin ciwon kalaman Aseem a ranta ya sassauta mata zuciyarta ya bata ikon yi masa biyayya koda zata cutu matuqar bata sabawa shari'ah ba
Da safe kuwa kamar yanda suka tsara hakance ta faru qarfe goma masallacin dake kusa da gdan Mal Hussaini ya dinke maqil da dandazon al'ummah saida aka fara daura auren Rabi'ah da angonta Mansur sannan na Dijah da Khamal sai na Asma'uh da Dr Aseem Shaheed nan gurin ya dauki kabbara maroqa suka rinqa zubawa angwaye kirari a cikin gdan kowacce amarya murna takeyi amma banda Asmah da tayi laqwas ta lafe jikin gado idanunta na saman silling hawayenta tun daren jiya yaqi tsayawa dukkan wata kalmarsa babu me dadin da zata tuna tasata farin ciki a daidai wannan Ikcn a ranta tanajin yanzu da bai rabata da Sadiq dinta ba da yanzu itama tanajin irin Happy din da yan'uwanta sukeji,  itadai haka ta yini bata iya tsinanawa kanta komai ba sai kuka ko kwalliya taqiyi qarfe Hudu kuwa motocin daukanta sukazo Ikcn daqyar Mal Hussaini yasata tayi wanka aikuwa tanajin ance ita akazo tafiya da ita ta rushe da kuka me dukan zuciya ta qanqame innarta tana mata magiyar kada ta bari a tafi da ita idan aka tafi da ita waye zaike yiwa Innah aikin gda,

Duk rashin tausayin Mudan ranar saida qanwar tasa tasashi kuka daqyar ya bambareta jikin Innah yasata a mota ya rufe tana kuka tana kiran sunansa shima hawaye yake sharewa hakan motocin suka daga suka dauki hanyar  Shagari quarters horn sukayi aka bude musu get Aunty Aseemah ta bude musu bangaren amarya Asmah har zuwa Ikcn shassheqar kuka takeyi sukuwa yan kawo amarya lalacewa sukayi a kallon wannan katafaren falo basu qarewa duniya kallo ba saida suka haura saman me dauke da madaidaicin falo da dakuna biyu sun bawa ido abinci sosai.
Dake ba yawane dasu ba kasancewar yace kada a wucce mutum biyar  haka suka zaunarta a saman carpet din dake tsakiyar dakin jikin gadonta suka farayi mata sallama suka fice hatta Jiddarh ficewa tayi tabisu aka barta ita daya tanata aikin kukanta me ban tausayi,  kusan awa

uku tana zaune ita kadai tun biyar har tara sannan taji tsaiwar mota a harabar gidan qirjinta ya buga da qarfi ta koma ta sake lafewa dukan qirjinta na qaruwa daidai lkcn da taji an bude qofar an shigo an sake murda ta dakin an shigo qamshin turarensa ya daki hancinta ta sake narkewa inda shikuma ya tsaya akanta yana qare mata kallo, yafi 5 minutes yana kallonta kafin yayi wani murmushi yace “waike nan kin yarda amarya ce ke ko? Hmmm yarinya kinyi kuskure babba da kika yarda kika fado komata tabbas zaki fahimci bambamcin da kika kasa ganewa, am ba bata lkc nazo ba ga wannan ki taba nasan qila rabonki da nama tun sallah sorry karki damu da sai kin biya bana buqata kasancewar qyanqyaminki nakeji, abu daya da zan fadanki shine idan kin tashi kullum da safe kinada aiki a gdannan, ki shiga wancan part din ki gyarashi sosai sannan ki samawa matata abinda zataci am tanada qaramin ciki ne bata aikin komai saboda tanada matsalar mahaifa tana buqatar tausa kuma batason ta inji so duk sanda ta buqaci tausa kiyi mata har sai tace ya isa haka ina fatan kin gane?".................

_*Oum Hairan*_
[20/06 4:32 pm] Oum Hairan: _*Zarrah*_

_*Fauziyyah Tasiu Umar*_

_*23-24*_

Juyawa yayi ya fice daga dakin yaja qofar ya rufe ta miqe ta bude labule tana kallonsa ya bude dayan bangaren ya shiga ya mayar ya rufe taja fasali tare da ajiyar zuciya ta koma ta bude ledar gasasshiyar hanta ce da taji kayan lambu sai qamshin takeyi dayar ledar kuma kaza ce itama ta hadu taja fasali ta zauna da farko kamar kartaci zuciyarta ta raya mata garama taci rabonta ne idan bataci bama ba gwaninta zatayi ba.
Sake budewa tayi ta dauki hantar takai bakinta saida taci iyakar cinta ta kora da lemon ta miqe ta cire mayafinta ta shiga bathroom ta bata lkc tana kallon bayin tana mamakin irin tsaruwarsa kafin ta dauki sabon brush ta bude ta matsi man goge haqori ta wanke ta cire kayanta ta fara kokawa da shower ta hada ruwa tayi wanka ta fito ta shafa mai ta bude wadroop din ta dauko doguwar rigar bacci tasa ta karkade gadon ta haye taja bargo tayi kwanciyarta.

Baccinta tayi cikin kwanciyar hankali saboda gajiyar biki bata farka ba sai safiya ta tashi tayi wanka tayi sallah tana saman sallaya taji an taba qofar ta juya ta kalli qofar jin shiru baa qara tabawa ba yasata tunanin babu kowa taxi gaba da lazuminta sake taba qofar ne yasata miqewa tana tambayar “waye" ba ayi mgn ba ta bude qofar taja da baya da sauri Aseem ne tsaye cikin shirinsa na tafiya aiki da tarkacen laptop da takardu a hannunsa.
 Qasa tayi cikin ladabi tace “ina kwana" Idanunsa ya dauke daga kanta ya juya ya fara tafiya saida ya kusa step din benen sannan yace “Mimee tana jiranki kije ki hada mata break" wani abune ya caki zuciyarta tana kallonsa ya fice hawaye suka sulalo mata na baqin ciki wannan baqin qasqanci da mahaifinta ya siya mata Allah wadarai dashi, komawa tayi ciki ta dauki wayarta da keta ring ganin number ya mudam tasan Innah keson mgn da ita ta kara a kunnenta a sanyaye,  yanayin yanda tayi sallama ya tabbatarwa Innah ba qalau ba taja ajiyar zuciya tace “ya akayine ma'uh na?" Cikin kuka ta durqushe a qasa ta kwashe duk abinda Aseem din ya fada mata ta sanar da Innah Sosai Innah ta girgiza dajin wannan qasqanci da rayuwar Asma'uh ta tsinci kai a ciki amma a fili sai tace “duk a cikin ibada ne kiyi hqr zakiga ribarsa a gaba don Allah badon niba ki mayar da komi ya zama ba komi ba koda anyi abinda ya kamata ki kalla ki kawar dakai wataran sai labari"

Cikin mutuwar jiki tace “yanzu Innah yimata zanyi?" Murmushi Innah tayi tace “qwarai kuwa yi zakiyi domin Allah ai lalura ta kori komai kema wataran zata taimakeki" haka inna ta rinqa tausar Asmah hardai ta hqr ta saki ranta ta miqe ta dauki hijjab dinta ta nufi part din Mimee ta qwanqwasa aka bata izinin shiga ta bude ta shiga cikin nutsuwarta me tsayawa a rai tayi sallama,  a qasan maqoshi mimee ta amsa tanajin wani kishi na taso mata duk yanda su Saimah sukazo suke koda kyawun matar yayan nasu ganin idonta sai taga tafi haka duk da kasancewar ba fara bace amma a sahun kyawu dole ta karbi lambar yabo.
Rusunawa tayi tace “Ina kwana Aunty...." Numfashi Mimee ta sauke tace “normal ina fatan Honey ya zayyana miki aikinki a gdannan ko?" Jinjina kai tayi Mimee tayi murmushi tace “ok sai a tashi a fara ina buqatar kunun tsamiya ne da qosan bread" miqewa tayi ta fara neman kitchen din ta nuna mata tace “ai basai kin wahala ba da part dinki da wannan duk iri daya ne bambamcin kawai a matsayi yake " duk da Asmah tasan mgn Mimee ta fada mata bata kula ba ta nufi kitchen din a hargitse yake gabadaya kayan sunyi qura ta jinjina kai ta lalubi tukunya ta dora ruwa ta rinqa bude kitchen cabinet din har allah yasa ta samu duk abinda take buqata ta hada ruwan kununta sannan ta debi surfaffen wake tasa masa ruwan zafi ya tashi ta hada tattasai da albasa da attaruhu da duk abinda tasan zata buqata ta wanke ta zuba a blander,  a wannan lkcn ilimi ne kawai yake aiki bawai sani ba duk kayan aikin baqine a gurinta hakanan dai ta ganganda ta gama hada komai ta Jere a dinning din ta koma kitchen din ta fara gyaransa saida ta gyareshi tsaf ta wanke kayan da sukayi qura ta mayar dasu muhallinsu sannan ta fita parlor shima ta gyara tayi duk abinda ya dace sannan ta juya zata tafi taji Mimee dake zaune

tana kallo tace “ki hau sama ki gyara masa dakinsa"

Tuni wani riqaqqen baqin ciki ya cika zuciyarta taji kamar tayi tafiyarta kalaman Innah ne kawai suka sata juyawa ta nufi saman ta bude dakin farko Allah kuwa ya taimaketa shi dinne ta shiga ta fara gyarawa saida ta gyareshi tsaf kayan da ya cire duk ta ninke tasa a kwandon zuba kayan wanki ta wanke bathroom ta fesa turare ta janyo ta fito ta rusuna gaban mimee tace “na gama" daganta kai kawai tayi ta juya tayi tafiyarta ta koma nata part din ta gyara ta nemawa kanta abinda zataci ta dawo ta zauna a parlor ta kunna kallo tana kallo tana karyawa bayan ta gama ta haura saman tayi wanka tayi kwanciyarta

Wayar tace ta dauki ruri ta daukota ta duba taja ajiyar zuciya Dijanta ce ta kara a kunnenta tayi sallama dijah ta amsa da sanyin murya tace “inanan inata tausayinki ance mazan da sukasan dadin mace sunfi rashin tausayi a daren farko Ma'uh nikam naci wuya ji nake kamar kar a qara" sarai ta gane inda ta dosa tayi dariya me qarfi tace “lallai inayi murna kice har Ali yaga Ali?" Ajiyar zuciya Dijah tayi tace “yanzu ke haka kuka kwana yana kallonki kina kallonsa duk irin maqudan kudadan daya kashe Allah bai fanshe ba?"

Numfashi taja tace “nifa banson gulmarki nan ina ruwanki  tunda kedai anyi miki abinda kikeso" sanin hali yasa Dijah cewa “kekam kin fiya masifa daga na kiraki mu jajantawa juna zaki kama yimin fada to ai shikenan sai kiyita yi nidai nazama cikakkiyar mace yarinya ko iyanan alamu sun nuna nafiki" murmushi tayi tace “to meye na gorin abinnan da ba dambe ba kowacce mace ma tana zuwa gurin Ikc dai igiya uku ke gareki nima itace dani saboda haka banga bambamcin ba".........
Kashe wayarta tayi ta gyara kwanciyarta tasha bacci sosai har wajen daya sannan ta tashi tayi sallah ta gyara gadonta ta nufi part din Mimee har yanzu tana kwance inda ta barta mamaki ya cika Asmah tayi mata sannu da gda ta dago ta kalleta saida gabanta ya fadi ganin irin kwalliyar da Asmah ta caba cikin wani tsadadden less dake cikin lefenta,  sarai take kallon Asmah tun daga sama har qasa ta zubawa hips dinta ido tuni Asmah ta fahimci kallon qurillar da takeyi mata tayi qaramin murmushi a ranta tace “jira dai madam ba damuwata mijinki ba amma dole ne kisan nafi qarfin matsayin da kuka ajeni"
Dagowa tayi tace “me kike buqata?" Iska Mimee ta furzar ta qanqance ido tace “kewai bakisan matsayinki bane a gdannan? Waye ya baki damar kwalliya?" Dagowa tayi ta dubi mimee tace “wai dake naji sunanmu daya a duniya Matan Dr Aseem Shaheed shiyasa nabawa kaina yancin kwalliya a gdan mijina....."

Wata muguwar tsawa mimee ta daka mata tace “Ubanwa yace miki matsayinmu daya dake yar matsiyata? Ke mece a mata da har zaki hada kanki dani??" Abinda Asmah takeso kenan ta juya cikin salonta na iskanci tana kada mata mazaunai tace “In kinga dama ma ki kirani da tafi haka nidai inajin kaina matsayin matar Mijinki bawai isar ki ce tasa na qudurta yi miki wannan aikin da kuka bani ba not sister tausayinki ne a matsayinki na patient kuma naji mijina yace cikine dake zaki haifa mana sanyin idaniya" tsayawa tayi ta juyo tace.
“Bari kiji wani abu ko Maryam naso ko bataso Asma'uh ta Aseem Shaheed ce zabinsa ce sannan inayi ne don farin cikinsa tabbas zanyi komai indai zaisa mijina abin alfaharina Happy domin nasan zamusha mango harda gwanda ke har water milon zan yanka nabashi a baki....."
Dafe kuncinta tayi da sauri ta dago sukayi ido hudu da Aseem dake tsaye, ya hade rai sai huci yakeyi maimakon tayi qoqarin yin wani abu sai kawai ta shammaceshi ta fada jikinsa ta qanqameshi ta rushe da kuka, raunin Aseem kenan A duniya baya qaunar kuka a cikin kukanma ya rasa masifar da tasa indai Asmah zatayi kuka sai yafi dagansa hankali fiye da yanda kukan kowa yake dagansa.
